Kusan 7mins yana zaune a mota shida Waleed yanama yaron wasa Waleed sai wannan hausan da yar turenci kadan dayakeji yake masa yana amsasa gogar bata fitoba, kofa yaji an bude hakan yasa yadago kansa dayake tinted ne glass na motan tsareta da idanu yayi bakinta is still showing signs na kumbura, idanun nan sunci kuka sunyi suntum but she still looks very pretty, zanin goyon Waleed ne kawai a hannunta, ganin key jikin kofan ta gaba yasa ta murza ta zare, bakinsa ne yayi motsi yana kallonta yace “stubborn girl!” Zagayowa tayi tabude motan Waleed yayi wani ihu akan jikinsa yana murna yace “Ummyy kalle” yajuya sitarin mota ta dauke kai batare data kulasa ba tamaida kofan tarufe, reverse yayi abinsa baice mata ci kanki ba Waleed sai murna yake yana tayasa tuki, saida suka shiga major road yasa hannu daya ya rungumesa gently ajikinsa yace “be good okay” gyadamai kai Waleed yayi yay lamoo ajikinsa, suna shiga asibitin Safeerah tashiga bin ko’ina da kallo idanunta suka ciko da hawaye sosai, parking yayi yabude motan yafito ko’ina a hospital din sojojine yana fitowa few sojas dake wajen suka kame suna saramai, da hannu yamusu alamu su bace yahade fuska Waleed sai kallon sojoji yake da uniform ajikinsu, fitowa Safeerah tayi ahankali ta maida kofan tarufe hakan yasa yawuce rikeda Waleed, lurada bata biye dashi yasa ya tsaya yadan juyo ya kalleta hada ido sukayi kiris take jira tafashe da kuka tana kallonshi idanunta suka kara cika da kwalla, anatse yajuya yacigaba da tafiya hakan yasa da kyar tadaga kafafunta dasukai sanyi tacigaba da binsa harciki wani daki taga yayi knocking ya dakata aka budemai kofan Mama tafito tana ganin Waleed a hannunsa yayi kyau sosai sanye da tufafi masu kyan gaske tace “laaaa Waleed ayoyo taho” tamika hannu cikeda kewan yaron zata daukesa kin zuwa Waleed yayi yamakalkale Salim sosai dadan sauri Safeerah tazo wajen ta rakube tana kallon Mama dataki kallonta

cikeda barkwanci tace “kayi babban aboki fa Salim” dan murmushi kadan yayi baice komiba, gaban Safeerah na faduwa sounding so guilty tace “Mama ina wuni” ko kallonta Mama batayiba tajuya tace “shigo Salim Bismillah” tafito ta matsamai gefe shiga yayi ciki Mama tama Safeerah wani mugun kallo haba sai kuka, Mama tanunata da hannu tace “idan banzo na mammakeki awajen nan ba basunana Maryam ba, Safeerah, Safeerah, Safeerah sainaci miki mutunci, kinci sa’a asibiti muke” Mama tajuya zata koma ciki dasauri Safeerah ta matso takama hannunta cikin kuka murya kasa kasa tace “Mama dan Allah kiyakuri wlh bazan karaba” “karya kike cikani, cikani, kuma bazaki shigo dakin nan ba wannan ne hukuncin ki wuce kujeranchan ki zauna kiyi tunanin abubuwan dakikayi da basu kyauta ba, sai kinyi realizing mistakes naki kin fadesu da bakinki sannan zanyi tunani idan zan hakura na yafemiki ko bazan hakura ba, cikani” Mama tajuya fizge hannunta tanuna mata chairs na zaman wajajen, wucewa Safeerah tayi ahankali taje ta zauna, Mama tace “good start evaluating your action mara kunya” tana maganan tabude kofa tashiga tsaf Salim yaji komi amman yayi kaman baisan abinda yafaru ba, yadubi Baba da oxygen ke hancinsa yana bacci yace “ya farka Mama?” Mama na daukan Waleed dayazo wajenta tace “eh ya tashi dazu sun kawo masa abinci bai iyaci ba sai suka basa orange juice ya shanye” gyadamata kai yayi yace “Allah kara sauki bari naje naga Dr Isa” Mama tace “angode Salim Allah yasaka da mafificin alkhairi” yamike tsaye Waleed ya zabura zai sauka daga jikin Mama tarikesa tace “dadina dakai bakasan ya isa ba ko Waleed, ba’a yawo a asibiti likita zaije gani kaji” raurau Waleed yayi da fuska zai fashe da kuka hakan yasa Salim yaji wani iri a ransa saiya kawo hannu yace “barsa Mama” tsare Salim Mama tai da idanu tasaki Waleed dasauri yasauke jikinta kawai yayi hugging Salim, Salim felt something da little hug da yaron na yaro saiya duka ya daukesa yace “ba inda zani don’t be sad” murmushi Waleed yamasa ya kankamesa, kofa yabude yafito Mama tabisu da kallo kaman wacce noticed something.

Yana fitowa yahada ido da Safeerah da idanun nan suka rine da kuka is true fa old habit die hard tun tun tana yarinya daman ta iya kuka yanzu ma still ta iya, aransa yace “stubborn girl” dauke kai yayi yaja kofa yarufe yawuce abinsa batare daya kara kallonta ba tafiya one two three yayi yaji muryanta. “Please kacema Mama tayakuri tabarni inga Baba” juyo da kansa yayi dasauri ta sauke kanta kasa tana wasa da yatsu, murya kasa kasa yace “why should I beg for a stubborn person when I know very well zaki karayin rashin kunyan” girgiza kai tayi tana goge fuska da bayan hannu tace “bazan karaba” tsayawa yayi yakalleta kukan ya isa haka shima yagaji da ganinta tun jiya tana abu daya one thing about Salim is baida kunya and he’s not just super bold he’s extremely bold, dauke kai yayi yawuceta yakoma wajen dakin Safeerah tajuyo dasauri ta kallesa kofan yayi knocking tareda budewa Mama dake zaune gefen Baba tadago kai tana sauke ijiyan zuciya dan tunani take, ahankali yace “Mama amata afuwa! Bazata karaba!” Mama na kallonsa tace “karya takemaka indai Safeerah ce saita kara” ta gefen idanu yaga Safeerah tazo wajen tadan rakube a bangon dake gefen kofan hakan yasa strictly yace “Mama duk randa takarama babba rashin kunya I promise dakaina zan umarci sojoji

suzo su dauketa akulleta gidan gyara hali!” Dawani mahaukacin sauri Safeerah ta kalli Salim dake kallon cikin dakin gabanta da kirjinta sun mugun bugawa, wanda yagama cewa ta aure sa ne zaisa a kulleta wato muguntan sojoji daban ne, Mama najin maganan tawani sauko daga gado tace “ubangiji Allah yamaka albarka Salim! Kai kai kai Alhamdulillahi yau ka farantamin rai, ina ja’iran hope tana jinka, ni dama kasa an tadı da ita yanzu an horata ta gyara halinta” dudda yanda idanunta suka kumbura saida ta kwalalosu sosai jin abinda Mama tafada, yace “Mama tace bazata kara ba kibata second chance amata afuwa bari naje” yajuya yawuce batare daya kalli Safeerah ba yana wucewa Mama ta leko ta kalleta tace “Allah yakawomin maganinki bazanji tausayi ba wlh duk randa kika kara zan badake akaiki gidan gyara hali” ahankali tace “bazan karaba kiyakuri” kwafa Mama tayi tajuya takoma ciki Safeerah tabiyota da gudu tai wajen Baba dake bacci ta rungume sa sosai sai kuka Mama ya watsamata harara dudda tabata tausayi Safeerah can be stubborn but abu kadan ke horata, she is sure maganan gidan gyara halin nan ya tsoratata tadauka da gaske suke.

Saida Salim yayi hanyar office na Doctor ya dakata da tafiya ya kalli Waleed saiya tsuntsure da dariya, dariya looks so wired a face nasa dan baisabayi ba the way fuskansa was looking da dariyan yasa Waleed ya kwashe da dariya, ganin yanda Waleed kemai dariya yasa ya gyara fuskansa yayi murmushi kadan yace “matsoraciya!” Abun really crack him up he can’t remember the last time yayi dariya haka, bude office na Dr Isa yayi yashiga.

Almost 10mins yayi an office din suka fito tare zuwa mosque yana rike da Waleed sukaje masallaci sukai salla suka fito yakalli Waleed yace “kanajin yunwa?” Gyadamai kai Waleed yayi hakan yasa yadaukesa yashiga dashi cafeteria na hospital din cake yasaya masa yabasa bayan ya budemasa yafito suka wuce cikin hospital din sallama yayi gaban dakin tareda budewa daga Mama har Safeerah kallonsu sukayi Waleed da kansa yake tafiya hannunsa daya rikeda cake yanaci while dayan hannun nasa Salim na rike dashi gently yace “jeka wajen Mama bari naje office” tsayawa Waleed yayi yakallesa saiya dakatar da cake din dayake ci yayi wani iri da fuska zaiyi kuka Mama ta taso ta daukesa tace “kaifa bakada adalci ko Waleed ka barsa yatafi aiki sainamaka bambooo” Mama tadanmai kallon tsoratar da yaro lamo yayi ajikin Mama sai kawai yafashe da kuka that is so deep wani yirrrrr jikin Salim ya dauka ganin yanda Waleed yafashe da kuka Safeerah ta sauke kanta kasa ahankali, Mama tace “laaaaaa kaga harda hawaye da gaske ne kukan nan yau” adan hankali Salim yace “Mama kawosa” Dasauri Mama tace “mance dashi katafi aiki abinka Salim zaiyi shiru” juyoda kansa Waleed yayi yakalli Salim wani irin kuka yake harda ijiyan zuciya yana hawaye dawani irin sauri Salim yamiko

hannunsa Waleed yataho dasauri daukansa yayi feeling very bad yaron na kuka yayi hugging nasa yajuya yace “shiiiii stop crying ya isa ya isa” yabude kofa yafice Mama tabisu da kallo zuciyan Safeerah yayi wani iri this cry confirms to her how much Waleed ke son mutumin nan, sai zuciyanta ya sosu ta tuna Abbati da shine yakamata Waleed nama kuka haka but he hates yaron tun yana ciki, wani tausayin Waleed yarufeta hawaye ya gangaro mata da sauri ta share Mama tace lurada ita but sai tayi kaman bata ganiba, suna wajen kusan 10min yakara knocking tareda bude kofa Waleed da kansa ya shigo rike da sweet da chocolate ga cake yamai waving hannu yace “babyeeee” shima Salim yace “byeeee” Mama tace “angode Salim sai anjima” wucewa yayi Mama ta kalli Safeerah tace “bazaki je kimai godiya ba” ahankali tamike dan bataso takara batama Mama rai, Mama tadauki Waleed itakuma tabude kofa tafito basa awajen dasauri tashiga tafiya tafito yana kokarin bude mota yaga tafito kallonta yayi saida takusan zuwa inda yake yabude motan yashiga yazauna, wajen window sa taje tasa hannu tai knocking, sauke glass kasa yayi kadan yamata wani kallo yace “get in bana magana da mutane awaje” yaja glass din sama abinsa bata ganin komi kuma, dan jim tayi sai kuma tajuya tazagayo ahankali tabude motan batare data kalleshi ba tashigo tazauna taja kofan tarufe, tasauke kanta kasa tashiga wasa da yatsunta ahankali, motan yayi shiru, chan tadago kanta tadan kalleshi ganin ita yake kallo da sauri tamaida kanta kasa kirjinta na dukan uku uku tacigaba da wasa da yatsunta murya chan kasa tace “thank you for everything” tayi shiru murya kasa kasa tace “Allah saka da alkhairi, Allah kara budi da matsayi da daukaka, thank you” dan lumshe idanu Salim yayi yabude har cikin ransa yaji dadi but yayi shiru, dan shiru tayi tanaso tayi magana but tana tsoro sannan she feels idan batayi ba kaman she’s taking advantage of him ne azamanin nan waye zai kashe maka kudi haka, ba’a tambayi Mama ko kwandala in this big hospital ba only mean yabiya komi, dan dago kai tayi ta kalleshi hada ido sukayi da sauri tamaida kanta kasa su wai sojoji haka sukeda kallo, tana wasa da yatsunta maganan na mugun mata wuyan fita tana kuma fargaban fadamai but haka tadaure amman tai kasa chan da muryanta sabida tsoro da shakkan sa tace “nawa ka kashe mana ni da Waleed dakuma kudin asibitin Baba? In sha Allah I will work hard and pay you koda kadan kadan ne, uhmmm nawa ka kashe?” Tai maganan ciki ciki wlh kalaman ma basu fito da kyau ba tsabagen tsoro dakuma fargaba, kusan two minutes taji shiru hakan yasa tadan dago kanta kadan faduwa gabanta yayi ganin wani mugun kallon dayake mata dayasa taji hanjin cikinta ya kada tamaida kanta kasa tawani yunkura dasauri takai hannu da gudu zata bude kofa ya danna lock wlh batasan sanda tace “kay…….kaya kuri idan maganata ta bata maka rai”dan daidaita muryansa yayi dan maganan datamai yabatamai rai yace “I will be back anjima da daddare for an answer game da maganan dana miki!” Gyadamai kai tayi not herself why is he insisting about auren nan ita she hates aure, kai tsaye yace “get out!” batasan sanda tabude motan da sauri ba har saida kofan yadaki next car dake wajen tafito da sauri tamaida kofan ta rufe, reverse yayi dasauri yabar wajen tabi motan da kallo idanunta sunyi ja sannan tawuce takoma cikin asibitin takoma tashiga dakin nurse tazo da takarda tabata tai signing tafice Mama ta kalleta sosai tace “meya ce?” Faduwa gabanta yayi jin tambayan da Mama tamata sai lips dinta

yahau rawa Mama ta tsareta da idanu ahankali tace “cewa yayi wai bayan an sallamemu mu koma gidansa daya kaini nida Waleed jiya dukanmu muyi zaman mu wai yabani gidan shine nacemai a’a banso” tai shiru Mama dake kallonta tace “sai yace mene?” Kallon Mama tayi batasan mesa gabanta ke faduwa ba murya chan kasa tace “yace tunda inada girman kai bazan amshi kyautansa ba wai zai aureki yabani gidan a matsayin sadaki yabani zuwa dare nayi tunani” Mama na kallonta tace “wani shawara kika yanke Safeerah?” Dasauri takalli Mama tace “Mama mesa kike min tambaya haka?” Mama na kallonta tace “aure nabiyu ne wannan kinada yancin zaban miji dakanki” bata fuska tayi tace “Mama ni bazan kara aure ba harna mutu zanyi tunani nasan inda zamuje idan an sallami Baba” Mama tadade tana kallonta sai bata kara cewa komiba.

[4/10, 4:48 PM] AMINA KABIR CAP: □LOKACI BAI KURE BA□

✍M SHAKUR

SUBSCRIBE PLEASE □

SOMETHING BIG IS COMING □□

https://www.youtube.com/@mshakur

EPISODE 24

Waleed shima bacci yayi dan yayi ciye ciyen nan Mama ta kwantar dashi kan lafiyayyen couch na dakin.

Motsi Baba yayi hakan yasa daga Safeerah har Mama suka taso da sauri Safeerah tai wajen muryanta yayi rauni sosai tace “Baba Baba kanajina gani nan” bude idanunsa Baba yayi ahankali yadan gani dishi dishi but he was able to know Safeerah ce murya chan kasa yace “Mamana kin dawo? Ina Waleed?” Fashewa da kuka Safeerah tayi kawai ta rungume Baba sosai tace “Baba kayakuri dan Allah, Baba baran karaba kayakuri I’m sorry kaji Baba, sabida nine rashin lafiyanka yatashi ko, baram kara tadamaka da hankaliba kaji Baba” hannunsa yadaga ahankali taredayin murmushi dan gaskiya yasami sauki yace “ai kaganta ga kiriniya ga iya kuwa, Feerah rigima, ya isa toh bar kukan haka” ya shafa bayanta Mama ta tsaya tana kallonsu kai Baba na son Safeerah bana wasaba to ko don ita kadaice yarsa oho amman baya wasa da Safeerah dagosa Safeerah tayi tana dago gadon ya zauna tace “meke maka ciwo yanzu Baba?” Girgiza kai yayi yace “ba abinda ke min ciwo Alhamdulillah inama dan gani baga Waleed chan ga kujera ba” yanuna Waleed dake bacci, Mama ya kalla yace “waya kawoni asibiti”? Yayi tambayan sabida yasan ba Mama Kubra bace wannan dake fushi dasu ahankali tace “Salim ne yakawo ka” shiru Baba yayi yana tunani yatuna sanda yazo yana masa maganan Safeerah daidai nan Dr Isa yazo Baba yaduba tsaf sannan yayi murmushi yace “bansan ko Major Salim ya gayamuku ba, inhar kanaso zaka bamu yardan ka muna kyautata zato zamu iya maka aiki a idanunka da sababbin technology mu dasuka shigo tsaf zaka iya gani, Major Salim yariga yabiya kudin aikin consent naka kawai mukeso dazaran BP ka yasauka sai ayi fixing time ashiga surgery Baba” tunda Dr Isa yafara magana kowa na dakin kallonsa yake especially Safeerah da kirjinta yahau bugawa batada burin da ganin Baba ya dawo, wayan nan idanuwan sune suka tankwafar da Baba yakasa samin sana’a muguwar yayarsa na yanda taga dama dashi, Baba yaje school yayi FCE he’s such a good teacher idanunsa suka dawo he can look for teaching job again har ranta taji dadi, Baba yadan kalli Mama sabida shi kudin ne aransa sai cin kudin Ogan yarsa suke but saiyaga Mama ta gyadamasa kai hakan yasa yace “to likita kunada consent dina a ina zanyi signing?” Wata takarda yasan karba daga hannun nurse ya matso yasa a hannun Baba yasamasa biro Baba yayi signing, Dr Isa ya karba yace “I will monitor you zuwa gobe idan BP ka yazama stable za’asa lokaci na aikin” gyadamai kai yayi yace “an gode likita, Allah saka da alkhairi” juyawa yayi yafice, Mama takalli Safeerah tace “kinyi salla wai ke yarinyar nan” girgizama Mama kai tayi, Mama tace “tashi kitafi masallaci kiyi salla” tashi tayi ba musu tawuce tabude kofa tafita ta rufo zata wuce saitaki ta tsaya dan yanda

Mama ta korata when she can simply pray adaki is somehow kunnenta tasa jikin kofan muryan Mama taji cikeda damuwa tace “Yayarka nata kiran wayanka Malam nasaka wayan silent banso yarka maraji tagane, sakon ta ya shigo ta aiko maka da sako a message” wayan Baba ya kalla cikeda damuwa yace “mita fada a sakon?” Shiru Safeerah taji Mama tayi sai chan tace “waya baka izinin shigomin dawani kato gida? Gidanka ne ko gidan ubanka ne? Gidana ake shigomin da wasu batare da izinina ba to bari kaji zumunci yaci uwarsa da ubansa tunda baku da godiyan Allah dakai da matarka kuma ku kama sahu kubi yarku ko kofar gidana kada ka kara zuwa inba hakaba saina maka wulakanci wanda harka mutu bazaka mantaba munafuki shashasha” Mama ta sauke ijiyan zuciya ta kalli Baba tace “yanzu ina zamu Malam? Ta ina zamu fara gamu da y’a, gamu da jika? Kano zamu koma da ake nemanmu akashe? Inamu ina zaman Abuja? Ko an maka aikin ma a ido kafin kasami aiki it takes time a zamanin nan damuke, bazan maka karyaba nadamu Malam” murmushi Baba yayi saiya rungumo Mama yanada danne damuwa yace “kidena damuwa ni nasan Allah bazai barmu ahaka ba, ya isa dan Allah karki kuka yarinyar nan tazo ta gane” wani kalan nauyi Safeerah taji zuciyanta yamata sai kawai ta tashi wajen kofan tawuce masallaci salla tayi tasa goshinta akasa takuma yi shiru kunya takeji tamayima kanta maganan aure after abinda tagani a auren, saita kasa rokon Allah komi ta taso kawai ta zauna har akai asir tayi sannan tadawo, tana bude dakin taga wani soja aciki yakawo basket dake dauke da manya manyan kulan abinci ga gwangwanin cerelac da madara a gefe aikin Salim ne, why is he so good to her? Meya yakemata alkhairi haka for mutumin da sau biyu sika hadu on Monday and Tuesday what is happening? Godiya Mama tama sojan yajuya yafita tabude kulan dan wlh yunwa takeji, tuwon shinkafa ne da miyan kuka mai kifi da kaza da man shanu, sai jellof rice da chicken tace “mezan sama ka Malam” ahankali Baba yace “tuwon yabani sha’awa” samai tayi ya karba yafara ci sai kallonsa Safeerah take Mama ta kalleta tace “ke bazaki ci ba” ahankali tace “anjima zanci” duk son abincinta dakuwa yamata yawa she loose apatite.

[4/10, 4:50 PM] AMINA KABIR CAP: □LOKACI BAI KURE BA□

✍M SHAKUR

SUBSCRIBE PLEASE

SOMETHING BIG IS COMING

https://www.youtube.com/@mshakur

EPISODE 25

Shi daman iyayensa sun sani ko yana gari baiwani cika zama gidansu ba sai idan yaga dama ko Ammi na kewansa he’s always fighting da Daddy so he’s avoiding him, gidansa na barrack yawuce bayan yatashi daga office, wanka yayi yasaka simple yadi brown jumper ce dinkin, Hermes slippers yasaka na maza yafito yana zuba uban kamshi, wata envelope dake kan table na falon yadauka yabude yaciro takardan yakalla sai kawai yamaida cikin envelope din yarike yafito yashiga mota, super market yabiya yayi sayyaya mostly for Waleed ne da irin kayan tea yasaka a booth yakoma gaba yawuce hospital wasu soja yabama kayan akai dakin ya tsaya yayi isha’i a mosque yayi magana da Dr Isa yana basa update kan lafiyan Baba.

Duk suna dakin Mama na goye da Waleed da akeso yayi bacci dan rigima yake saiya fita waje wasa yamafara gyangyadi while Safeerah na magana da Baba akai knocking Mama tawuce tabude kofa soja ne yashigo da uniform da leda yace “good evening Oga yace na kawo he’s coming” ya ijiye yajuya yafita Safeerah tai shiru tana kallon kayan kaman yanda su Baba keyi tace “zan maidamai abun yayi yawa”

Baba ahankali yace “ke kul babu kyau maida kyauta” bata sake magana ba almost 20mins akai knocking tareda sallama gabanta kawai yafadi jin muryansa, Mama tace “shigo Salim” bude kofan yayi yashigo Safeerah takasa kallonsa ya gaisa da Mama yama Baba yajiki, Baba yace “Salim dawainiyan nan batai yawa ba? Toh mungode Allah amfana, nagode kwarai Allah ya saka da mafificin alkhairi” kansa yasauke kasa yace “Allah kara lafiya Baba, kadinga cin abinci akai akai sannan karage damuwa Baba, duk batada amfani” Baba kadakai yana yabawa da natsuwan Salim da hankalinsa yace “ba shakka haka maganan ka take Salim, Allah yayi albarka” anatse Salim yace “tom Allah saida safen ku Allah baka lafiya Baba” sosai Baba yaji dadin addu’an yace “Ameen Ameen Salim nagode sosai” juyawa yayi yasaci kallon Waleed dake bayan Mama karaf Mama ta lura murmushi tayi tace “abokinka yayi bacci da yanzu yafara binka” sunnar dakai kasa yayi yace “saida safen Mama, zanzo gobe da yamman In sha Allah” Mama da Baba sukamai godiya, Baba shi kawai y□LOKACI BAI KURE BA□

✍M SHAKUR

SUBSCRIBE PLEASE □

SOMETHING BIG IS COMING □□

https://www.youtube.com/@mshakur

EPISODE 28

Saida aka shigar da Baba operation room sannan yabar Mama kadai awajen yafito shi baije wajen masallacin ba but daga inda ya tsaya yana hango masallacin.

Hangota yayi tafito daga masallaci she is still with that hijab, day 3 kenan she's still wearing the same thing stubborn girl, eyes nata sun sabe today but har yanzu basu gama washewa ba saida tafito tajuya tai wani dan karamin murmushi tamikama Waleed hannu alamun yazo da sauri yakama hannun yana wasa slippers nata tasaka tajuyo tafara tafiya out of nowhere wani mutum haka yatare gabanta yaga yana mata magana hakanan Salim yaji abu just hit his heart, kuma sai yaji zafi sosai kaman ciwo does he have heart problem ne? Ya tambayi kansa saiya juya zai koma ciki ina yaji in all levels yakasa kawai saiya juyo yasake kallonta bawai murmushi take ko magana ba but ta tsare mutumin dake mata magana da manyan idanunta ko kyaftawa batayi amman shi bata iya kallonsa haka kawai yaji bazai iya daurewa ba cike da izza yashiga tafiya one one kaman daga sama suka gansa awajen gaban Safeerah ya tsaya yama mutumin wani mugun kallo yace "lafiya!" Wlh ayanda muryansa yafito ba mutumin kadai ba har ita Safeerah saida gabanta yafadi gashi yamata wani babba agabanta sosai, adan daburce mutumin yace "tambaya nakeyi daman kan war……" "meya sami securities dinchan dabaka tambayesu ba kana tambayan matan aure!" Dasauri mutumin yace "ayakuri yallabai, ayakuri Oga" yajuya da sauri yawuce daidai Waleed nawani irin dirlowa daga hannun Mamansa yakama hannunsa yace "ayoyooooo" juyowa yayi yakalli Waleed dakawai ganinsa yasa yaji bacinran yabace dan karamin smile yasaki yace "Hello Finest boy Waleed, come here" yawani daukesa ya rungume yana kallon Safeerah daharta sauke kanta kasa, murya ciki ciki tace "ina yini" bata jira amsar sa ba tawuce dasauri ta tafi ta shiga ward din binta yayi da kallo she still walk kaman da.

7 aka fito da Baba an saka bandage a fuskansa.

Yana asibitin har isha'i awajensa Waleed yayi bacci sannan yadawo dashi yamusu sallama yatafi koda Mama tace taje tamasa sallama fitowa tayi but taki zuwa chan tadawo daki, kallonta Mama tayi tace "zo Feerah" zuwa tayi ta zauna gefen Mama, hannunta Mama ta kama tace "Salim yagaya miki waye shi?" Girgizama Mama kai tayi alamun a'a, ahankali Mama tace "dazu kina masallaci Babanki ya tambayesa mesa yake taimakon mu, shine yake gayamana shine mutumin da kika taimaka kika boye lokacin nan!" Tunda Mama tafara maganan kirjin Safeerah ke bugawa none stop, Mama tace "yanuna ma ni da Babanki hannunsa gabaki daya hannun tabon kunane haryau bai dawo daidai ba" wani irin kallon Mama Safeerah take, murmushi Mama tayi takai hannunta ta kama fuskan Safeerah tace "yace yanemeki sama da

kasa bai ganki ba not until rannan dakikazo company sa aiki” Mama tai shiru tace “ni da mahaifinki mun aminta da auren mun yarda, and mun yanke shawaran zamu shiga gidan tunda sadakin ki ne, da kyautane da munji wani iri, ga idanun Babanki anyi aiki yana warkewa zai nemi koyarwa we will live good babu wanda zai kara zaginmu, abinda nakeso dake yanzu is kidage da addu’a, Allah yasa Albarka a auren, Salim ba yaro bane abinda yasa muka karajin natsuwa dashi kenan, thank you Safeerah for saving us” Mama tayi rungumeta kankame Mama tayi tunani sunmata yawa aka daman shine mutumin nan? Saisa yadinga kallonta the first day daya ganta in his company, daman shine? But yanzu yafi girma.

**

Yau kwanan Baba five a hospital din Alhamdulillah yaji sauki ras idanun dazu aka bude da safe yana gani ras saidai sun kankance but Alhamdulillah, tun after rannan operation din Salim baizo ba sabida wani work trip daya tafi to France na just 3days but kullum yana aiko sojoji akawo musu daily need, yasayama Safeerah 5abayas yabada akaimata saida Mama tai da gaske sannan tasaka kayansa.

Yau aka sallami su but Dr Isa yace Salim yace ajirasa zaizo yakaisu gida duk suna zaune, Safeerah tasaka daya daga cikin abayan daya sayamata black yanada stones yamata kyau ajiki sosai dankwalin abayan ta yafa, Waleed short ne ajikinsa na jean dawani blue riga mai kyau da takalmi yayi kyau sai wasansa yake a tsakar dakin sun hada komi nasu tsaf, suna zaune akai knocking tareda sallama hakanan gaban Safeerah yafadi jin muryansa dasauri ta gyara gyalen kanta da kyau tana rufe gashinta, Mama tabudemai Waleed na ganinsa ya jefar da Cheese na hannunsa yadaga hannu yazo dagudu yace “ayoyooooo” daukan Waleed yayi dasauri yayi murmushi kadan yace “Finest Boy Waleed” kankamesa Waleed yayi Mama tace “ai sai ka barsa ko hannunka duk cheese zaka bata masa kaya” dasauri yace “Mama barsa bakomi” yashigo dakin batare daya kalli Safeerah da kanta ke kasa ba yayi wajen Baba yana mika masa hannu cikeda respect yace “Abba ina yini, idanu sunyi kyau” Dan dariya Baba yayi yana feeling very free with Salim yace “ai saiyau nake ganin ka da kyau, Salim kam Masha Allah” dan sunnar da kansa kasa yayi maganan Baba tasa yadanji kunya kadan yace “bari nasa akai kayan mota sai mu tafi” yajuya yakalli kofa yace “come in Boys” sojoji guda biyu suka shigo suna daukan yan kayansu Mama tazo inda Safeerah take zaune kan kujera, duka ta dakamata a sace Safeerah ta kalleta da sauri, wani harara ta mata irin bata iya gaisuwa ba, adan hankali Safeerah tace “ina yini” batare data kalleshi ba, shima bai kalleta ba yace “lafiya lau” yace “Abba Bismillah muje” Baba yace “asibiti ba dadi jama’a” yasauka ahankali yake tafiya Salim dake rike da Waleed na je rawa dashi suka fito, Mama ta kalleta tace “ke da bakin hali baki iya gaisuwa ba ko” kaman zatai kuka tace “Mama magana fa yakeyi saisa ban iya nai gaisuwan ba fa” Mama tace “muje mai kunnen kashi” murmushi tayi suka fito itada Mama.

Sunakai wajen motan ijiye Waleed yayi akasa shiya rike Baba cus baida karfi sosai yasaka sa abayan mota Safeerah da fitowansu kenan tareda Mama tadan saci kallonsa he’s so gently da mahaifinta, Mama ma tabisa da kallo sai tadan sauke ijiyan zuciya wlh she loves Salim for yarta sosai, karasawa wajen sukayi itama ta shiga baya, adan kunyace Safeerah tashiga gaba, shima yashiga Waleed na jikinsa ya kunna motan yaja har zuwa estate din Baba da Mama nata kallon ikon Allah sabida basu dauka a irin waje haka yabawa Safeerah gidaba, wlh estate din yafi GRA su Momma kyau sau dari, ga gidajen iri daya sak, saima dayayi parking gaban wani hadadden gida ga flowers anyi decorating wani mini garden, ga bike na yara da ball yasa awajen wanda she is sure bata gani the other day ba, yanzu wannan hamshakin gidan Safeerah ta karba jama’a? Kashe motan yayi yabude yafito yazagayo ta bangaren Baba yabude masa kofa, fitowa Baba yayi Mama ma haka, itama Safeerah jikinta yadan mata wani iri amman tadaure tabude motan tafito taciro key dake yar jakan hannunta ganin ko kallonta Salim bayayi wasa yake da Waleed abinsa yasa tai wajen kofa su Baba na kallonta tabude tajuyo ta kallesu saikuma takasa magana, Salim yace “mushiga ciki Abba” shiga Baba da Mama sukayi duk suna kallon gidan this is the moment of disbelief awajen gidan nan nasune yanzu? Su? Suka zauna afalon dayake a gyare, Salim yasauke Waleed yace “remember don’t cry zanje office okay” gyadamai Waleed yayi, gently yace “je Ummi tasa maka cartoon” dan satan kallonsa Safeerah tayi jin abinda yafadi yamike tsaye yace “sai anjiman ku Abba” har yayi kofa Baba yace “Salim” dasauri Salim yajuyo yace “na’am Baba” ahankali Baba yace “gobe kazo da magabatanka adaura muku aure ba amfanin bata wani lokaci tunda nasami lpy” faduwa gaban Safeerah yayi sosai jin abinda Baba yafada, Salim yadan gyadamai kai yace “toh Abba”.

MASON SHIGA GROUP DIN MU NA FINAFINAN AREWA 24 ON DEMAND

Su tuntube wannan number

08129756419[4/13, 3:38 PM] AMINA KABIR CAP: LOKACI BAI KURE BA

✍M SHAKUR

LOKACI BAI KURE BA ON YOUTUBE

DONT FORGET TO HIT THE SUBSCRIBE BUTTON

https://youtu.be/XTagsgVWdUw?si=9ZhBLwm8U1KRstEj

EPISODE 29

Wani haske kalaman Baba sukasa yaji aransa, deep down yanaji kaman yawani fizgo gobe tayi, he just wanna hear those golden words an daure tsakanin Salim Ibrahim Maradi da Safeerah Shu'ibu, rabonsa da gidansu yau kwana nawa dayana France ko sau daya Ammi bata kirasa ba maybe Dady yafada mata, sai kawai yawuce gidansu, parking yayi yafito flat nasa yawuce shower yafada tun yana ciki yaji wayansa na kuka karasa wanka yayi yafito jin wayan na kuka again yasa yatafi wajen wayan, ganin Ammi ke kiransa yasa yadaga wayan muryanta ba dadi kwata kwata tace "kazo ina dakina" bata jira amsawan sa ba ta katse wayan, ijiye wayan yayi shima yacigaba da shiryawa, wani 3quater yasaka wando yasaka, yasa t-shirt mai dogon hannu, slippers yasa sai kamshi yake yafito, flat nasu yashiga yaga Lubna da Ameera a falo suna tattare souvenirs dasuka hada na bikinsa dasauri sukace "sannu da zuwa Yaya" wucewa yayi bai amsasu ya gyadamusu kai ganin abubuwan dasuke hadawa yasa yatuna da auren da za'amai yawuce dakin Ammi yayi sallama yabude dakin Ammi ya shiga, Auwal yagani aciki da Layla kanwarsa datai aure yarta daya Meenal, Ammi yagani tahade rai sosai tana kallonsa, Layla tamike da murmushi sosai kan fuskanta tace "Yayaaa yau kwana na biyu ina gida banganka ba wayanka baya shiga" hancinta yaja yayi murmushi yace "i was in France" Auwal yace "ya hanya Yaya"? Anatse yace "Alhamdulillah" yana tahowa cikin dakin rike da Layla data basa side hug yasami waje yazauna yakalli Ammi yace "ina yini Ammi" Ammi bata amsasa ba sabida yanda ranta yake abace tace "kullum rannan duniya complain na mahaifinka is baka girmamasa, bakada respect menene menene, I see complain nasa baseless kawai yacika korafi ne but slowly na soma yarda da maganar sa yanzu" tai shiru, cikin tsantsan bacinrai tace "me nakeji haka daga bakin Dadynku Salim?" Dan lumshe idanu yayi yabudesu yace "me yaran nan keyi anan Ammi"? Yayi maganan yana musu wani kallo hakan yasa duk suka tashi

zasu fita Ammi tace “nina kirasu kudawo nan cus enough is enough” tsayawa duk sukayi Auwal yazauna kan hannun kujeran da Salim ke zaune kai din, Layla tazauna gefensa ahankali, Ammi tace “wat kind of embarrassment is this Salim? Few days to your wedding, gobe zasu fara events one week to wedding, Bazawara zaka auro ana zaune lafiya harda d’a fa?” Sauke kansa yayi kasa, Ammi tace “I’m talking to you kamin banza menakeji me hadinka dawata bazawara datazo IT company? Because she saved you and so?” Da dan zafi kan muryansa yace “wat if sonta nake Ammi? Wat if all this years I’ve fallen for her tun sanda ta taimakamin I’ve beeen searching for her? Dan naganta yanzu ta taba aure tanada yaro does that change anything Ammi? I am a Man yaushe karin aure yazama wani laifi ko wani abu? What am I doing wrong Ammi”? Cikin fushi Ammi tace “everything you are doing is wrong Salim, mahaifinka daya hada auren nan zaka kunyata? And yes it does matter sabida you are too small ka auri bazawara not to even mention ta taba haihuwa bayan ga budurwa wacce bata taba aure ba ce zaka aura” dan runtse ido yayi he hates d name da ake referring Safeerah dashi, Ammi tace “inba magani tamaka ba ga budurwa zaka aura yarinya danya shakap yau biki saura kwana takwas kace kai bazawara zaka aura kuma”? Ahankali yadan dafe kansa dake sarawa yace “wat do you want yanzu Ammi? Why did you call me here”? Cikin fushi Ammi tace “kabar maganan wani aure, Salim ran Babanka yabaci sosai, already kullum cikin damuwa nake da yanda baku jituwa kaidashi kun dawo goshi da keya, ka kama kai auren nan he will never forgive you, saisa na kira kanninka su saka baki, don’t ruin relationship dinka da Mahaifinka sabida wannan auren kaji Son” Ammi tadan sassauta murya tace “I hate yanda baku jituwa dakai da mahaifinka please respect his wish, give this girl kome takeso ka rabu da ita and face Nana Khadija kaji” ahankali Salim yace “I can’t Ammi!” Ba Ammi ba har kannensa kallonsa sukayi, Ammi tace “ni kake gayama you can’t?” Ahankali yace “da ace zan iya da tun last five years na hakura da nemanta, not a day goes by da banayin tunaninta, now that I’ve finally seen her kuma I can’t let her go, I’m really very sorry Ammi but I can’t grant this wish naki, Daddy needs to accept I’m a man, and I own my life, he should respect wish dina and yadena dictating mini my life! I am 39 Ammi not 13” yamike tsaye yajuya zai fita Ammi cikeda mamaki Salim tace “Salim!” Tsayawa yayi chak batare daya juyoba, Ammi tace “tun yanzu kafin ka aurota kafara nunamin ban isa ba ko?” Wani iri yaji sosai ahankali yace “baku taba kawo abu kuce nayi nakiyi ba, even Nanah ban muku gardama ba dakukace na aureta, but ni nakawo kunce a’a, and it’s too late nariga nabiya sadaki! And gobe za’a daura auren so I can’t back out now!” Kowa na dakin kallonsa yake da mugun mamaki ran Ammi ya matukar baci dataji yarinyar ma zai fara aure before Nana, da kyar ta daidaita muryanta tace “okay shikenan kaje kai aurenka dayake zabinka but kasani ba yawuna ciki, and as long as ina raye ni matarka daya nasani Nana Khadija, bazan taba accepting koma wace yarinyar da zaka auro ba” shiru yayi yay jimmm maganan ta tabasa sai kawai yabude kofa yafice daga dakin Layla tai wajen Ammi da sauri tace “Ammi please calm down dan Allah, Yaya baitaba disobeying dinku ba, ku fahimce sa kadan, haba Ammi kinfi Dady fahimta fa kinji Ammi na” Ammi da ranta yabaci tace “karki gayamin maganan banza Layla” ahankali Auwal yace “but Ammi Layla is right, Yaya

baitaba gardama da ku ba, even though bayason Nanah I saw it but ya yarda sabida zabinku ce, ni banmasan Safeerah ce yarinyar ba but rannan daya ganta naga yanda yake kallonta, bantaba ganin Yaya yakalli wata mace aduniya like that ba wlh, ku barsa ya aureta, Ammi tsakani da Allah bai kamata kuna gayama wanda is approaching 40 wat do and wat not to do ba, yanzu idan kuka hanashi aurenta shaidan ya shiga ransa da aurensa yaje yanabin yarinyar fa eh Ammi? Kunada kason zunubi, kidena biyema akidan Dady dan boko bayason aure aure, as long as zaiyi adalci, he's capable bamu zamu tayasa ciyar da su ba let him have his way, Ammi badan yarinyar nan ba da yanzu kullum muna kukan rashin Yaya yarasu? So koma menene he owe her his life Ammi kinji" shiru Ammi tayi jikinta yayi sanyi tace "Nanah fa? That girl is so innocent she's just 25 ina zata iya dawata bazawara? How will she feel 7days to bikinsu rannan da ake event na kauyawa day wanda zata aura na chan yana auren wata eh, Small girl zai aurowa Bazawara" Auwal yace "to ai Nana ta girmi Safeerah ma Ammi, Safeerah is just 20, kuma Nana tafi Safeerah girma da wayewa da komi ma babu wanda zai cutar da Nanah" Layla dake shafa Ammi tace "toh kinmaji Ammi calm down, yariga yasa ransa look at how serious he is da maganan so unlike Yaya, kika hanasa zaiyi abinda dukanmu bazamuji dadi ba, Ya Salim ba yaro bane let's respect him Ammi please, and ki lallaba Dady, stop supporting Dady blindingly let's call a spade a spade Ammi" shiru Ammi tayi tana kallonsu saikuma tace "dallah kutashi daga gabana munafukai kawai" ta watsa musu harara Auwal yafice Ammi is kind laslas she will come around, Dady ne dan bala'i Layla tabisa abaya suka fice, flat din Salim suka shiga baya falo sama suka wuce knocking Layla tayi gaban dakinsa tace "Ya Salim" murya ciki ciki yace "wat" gently tace "can we come in? Ni da Ya Auwal ne, mushigo"? Shiru yayi chan yace "come on in" bude kofan tayi ahankali ta shiga yana zaune bakin gado wucewa tayi ahankali ta zauna kusada shi shikuma Auwal yazauna kan kujera, ahankali Layla tace "Yaya you're the best brother I trust with my own life, I know you Yaya, you are such a critical thinker, bakada garaje, kome zakayi nasan bazaka taba abunda zakai bringing shame to our family ba, I don't care idan mata hundred zaka aura you have my support, nasan zakai adalci Yaya, Ammi will come around i promise Dady ne dai sai Allah" shiru yayi yana kallonta saikuma yadanja hancinta yace "remind me how old is this girl again Auwal"? Murmushi Auwal yayi yace "28yrs" Salim yace "and she's this smart are you sure bazan gayama Habib yakaro kudin sadakiba wanda yabiya abaya yayi expire" dariya sukayi Layla kawai ta rungume shi tace "I just love you Yaya so much and I trust you, I trust your decision, you deserve Safeerah! A selfless girl mai taimako da jarumta da kirki only deserves a selfless Man mai taimako da kirki like you" bayanta ya shafa calmly yace "thank you Layla" anatse Auwal yace "but Yaya just from kawota wajena da Shamsu yayi is like akwai issue a family su he treats the girl like trash at a point saida namai magana ma nakasa daurewa" dan shiru Salim yayi gently yace "that's why I wanna take her away" yayi shiru chan sai ya gayamusu komi dake faruwa yace "that's why I wanna keep her by my side, she kept me hidden then even though nace zan tafi" murmushi Layla tayi tace "Yaya zan iya binku gobe idan zaku?" Gyadamata kai yayi yace "yes! Baffa zai bini ko bazai bini ba I'm not sure but i called him, sai Kabir KB da mahaifinsa

incase Baffa bai bini ba” Auwal yace “zani nima” gyadamusu kai yayi sai suka zauna dashi he was sad actually sabida Ammi but sunsa almost 70% na damuwansa is gone.

**

[4/13, 3:38 PM] AMINA KABIR CAP: □LOKACI BAI KURE BA□

✍M SHAKUR

LOKACI BAI KURE BA ON YOUTUBE

DONT FORGET TO HIT THE SUBSCRIBE BUTTON □

https://youtu.be/XTagsgVWdUw?si=9ZhBLwm8U1KRstEj

EPISODE 30

Babu wani kayan abinci da babu agidan, everything ansa agidan, hankalin Safeerah yawani irin kwanta ganinta da iyayenta cikin gidan, Baba da Mama sun saki jikinsu sosai they’re very happy wlh, babu abinda yakai runfa akanka taka babu mai zuwa ya zageka ko yacimaka mutunci.

Safeerah tadafa lafiyayyen abinci tanaso taje ta kwaso kayanta agidan nan da komi nata but batasan yazatayi ba haka dai har washegari girki sukayi itada Mama na tarban bakin ita batada number sa yakira Baba yace zasuzo shabiyu, Baba yakira wani amininsa yamai kwatancen gidan yazo tacema Mama zataje gidan nan ta kwaso kayansu tafice bata saurari Mama ba layin taje gabanta sai faduwa yake asace ta tura gaban gate tashiga ba kowa compound din wuf tafada dakinsu na gateman, ghana masgonta da credentials nata ta sunkuta dana Waleed dana Mama da Baba duka tafito dasu tafara kaiwa waje one one keke na tayata sawa daidai

tadauki na Waleed Salma tafito tace “sata kikeyi”? Safeerah tace “bakuda abunda zam sata” tadauki jakan zata fice Salma ta fizge tace ai mu muka sai kayan ki barsu anan” kallon Salma Safeerah tayi batason rigima ga gidan gyaran hali data tuna saita barmata tajuya tafice fuuu tashiga keke yaja sukabar unguwan har layinsu da kyar estate din suka bari keke ya shiga.

Wuraren 11 tafito daga keken yatayata sauko da komi tana shiga dasu Mama kawai ta kalleta bata cemata komiba, sama sukakai komi Mama tawuce ta chanza kaya tasaka atampa mai kyau da babban mayafi, Baba ma ya shirya cikin shaddarsa mai kyau duk daga kayan da Safeerah ta kwaso musu, itakuma tasake wanke dan tayi zufa tasaka normal gown nata tasaki kanta danyasha iska tajika tai kwanciyarta tanaji anyi baki gabanta yafara faduwa.

Aminin Baba yamusu iso falon, Baffa yafara shigowa dawani abokinsa, sai mahaifin Kabir, sai Auwal da Layla data saka wani lafiyayyen lace, sai Salim yasaka shadda mai kyau fara kal tareda KB, duk zama sukai afalo aka gaggaisa Waleed dasauri yaje wajen Salim yadaukesa sai wasa suka da yaron barinma Layla dan Waleed akwai kyau gasa tuluki kuma yasa kaya masu kyau, anatse Layla tace “Mama ina Safeerah”? Murmushi Mama tayi tace “muje tana sama” takarbi Waleed tace “taho Waleely kagani” suka wuce sama ko kadan Safeerah batasan za’a ganta ba Mama kawai tabude dakinta tace “Safeerah ga yar uwarki tazo ganinki” dawani irin sauri Safeerah ta tashi daga gadon Layla tabi uban gashinta da kallo tai wani murmushi tace “Safeerah!” Akunyace Safeerah ta sauke kanta kasa tarasa abinda zatayi sai kawai ta duka tace “ina yini” dasauri Layla takamata tace “laaa mehaka yar yarinya dani kina dukawa ki gaidani, tashi” tashi Safeerah tayi ahankali akuma kunyace tawuce wajen ghana masgon dake wajen tajawo wani gogaggen hijab tasaka Layla na mamaki wlh da za’ace budurwa ce zata yarda batai kama da wacce zata haifi Waleed ba and she’s damn beautiful, like extremely beautiful, ga flat tummy kaman bata haihuwa, ga hip ba chanchan sosai ba but yafi hips nata girma, ayanda ta ganta ko bra bata saka ba yarinyar akwai boobs manya a tsaye kaman Waleed baisha ba, ga gashi, ga idanu farare tass, ga pink lips, ga gira, the only abu da Nanah zata nuna mata is hasken fata wlh dakuma girman shekaru, da tsayi, sannan Safeerah nada natsuwa sosai ga kunya, unlike Nana that is lively akwai hira, dawowa tayi ta zauna akasa still kunyanta takeji tace “mezan kawo miki”? Dariya Layla tayi tace “wai kinamin haka haka kaman kinga Ammi mother Inlaw naki gabadaya, nasha ruwa a falo besides ai bazaki iya sauka bama maza na falo, sunana Layla ni sister Yaya Salim ce, nike bin Ya Auwal sai Ameera da Lubna, thank you for helping Yaya lokacin nan, my family is grateful” sunnar da kanta kasa Safeerah tayi batai magana ba, Layla tace “bazaki min tambayoyi kan mijin naki ba”?

Sake sunnar da kanta kasa Safeerah tayi kunya takeji Layla tace “ai shikenan” ta gyara zama tace “kinga Yaya yanada kirki na bala’i amman bayason raini yanada fushi aka tabasa, sannan halinsa nada wuyan ganewa yanada wuyan ka karantasa amman he’s easy going wlh, he is into diet so yanason healthy meals, bayason soye

soye ko oily abu, he love vegetables, fruits, da proteins, Allah yasa albarka a aurenku yakada fitina”….

Baffa yace “nine yayan mahaifinsa, due to some unforeseen reasons Allah bai bawa mahaifinsa daman zuwa ba, ga Aminina, mahaifin Babban amininsa Kabir, ga kaninsa Auwal, sai kanwarsa Layla, danmu yamin bayani sun riga sun daidaita zancen sadaki da Safeerah ko”? Baba yace “kwarai” Baffa yace “to za’a bamu aurenta yau ne ko akwai abinda kukeso ayi” Baba yace “adaura yanzu mun shirya” nan take aka daura auren Safeerah Shu’ibu da Salim İbrahim Maradi akan sadaki wannan gida aka shafa anata addu’a ana samusu albarka, wani boyayyen ijiyan zuciya Salim ya sauke da saida KB ya lura, he’s feeling kaman finally yabawa zuciyansa abinda yadade yana nema, yaji wani sanyi aransa, dawata natsuwa, da contentment”

[4/13, 3:39 PM] AMINA KABIR CAP: □LOKACI BAI KURE BA□

✍M SHAKUR

LOKACI BAI KURE BA ON YOUTUBE

DONT FORGET TO HIT THE SUBSCRIBE BUTTON □

https://youtu.be/XTagsgVWdUw?si=9ZhBLwm8U1KRstEj

EPISODE 31

Mama tai shiru like shikenan Safeerah tai aure, wannan aure ne da su sukamata ba wanda aka mataba a chan gidan ba, har kasan ranta takewa yarta addu’a Allah sa this aure should be the best for her. Sunci abubuwan da aka kawo har cupcake Safeerah tayi, Salim ne kawai baici abu sosai ba dan he is really overwhelmed so cikinsa yacika, sallan azahar sukayi anan falo akai jam’i sannan akai sallama za’a

tafi, Mama tace “bari na kira Layla” wucewa Mama tayi sama tasami Layla adakin daketama Safeerah hira tana bata labarin duka yan gidansu tace “zaku tafi Layla” tashi tayi tace “tom Safeerah saimun sake haduwa ko” mikewa Safeerah tayi wlh kawai kunyan Layla takeji ta gyadamata kai tace “tom nagode sosai Anty agaida Meenal da kowa” hannunta Layla takama ahankali, hannun Safeerah taushi kaman na karaman yarinya tace “tom byeee” sannan tasaketa tawuce tafito suka sauka kasa tareda Mama, babu kowa a falon waje tafice sai chan tashigo tazo wajen Mama tabata wata yar jaka tace “gashi yace abawa matarsa” atare daga Mam har Layla sukai murmushi, karba Mama tayi tace “tom zan bata kuwa yanzu, agaida yara dakuma Mama Layla” Layla tace “zasuji Mama bye” tawuce tafita Mama takoma sama tasami Safeerah zaune kan gado yarinyar duk tai wani iri Mama ta ijiye jakan gefenta tace “mijinki yace akawo miki” ko kallon jakan batayi ba sai gyadama Mama kai kawai datayi ahankali Mama ta zauna gefenta ta kalleta tace “menene Safeerah?” Girgizama Mama kai tayi tace “bakomi Mama, kaina naji yanadan ciwo kawai” hannu Mama takai takamo kafadanta hakan yasa gently takai kanta tadaura kan kafadar Mama wani natsuwa taji saita sake gyara zama kawai ta kankame Mama, wani irin sassanyar kuka tasaki da batasan ma daga ina yazo ba, Mama tace “ke a aure na biyun ma still kuka zakiyi” cikin kuka tace “Mama bansan mutumin nan ba, bansan komi akansa ba, satin nan na sansa, satin nan na auresa, Mama wlh banason nakuma aure na tsani aure, maza basuda kirki, all abubuwan nan dayakeyi idan he is worst than Abbati fa Mama? Bansan komi kansa ba, zai yarda Waleed ya zauna gidan? Idan ya yarda yanzu daga baya yace yaron yabar gidansa fa? Mama rike d’a wanda bakai ka haifesa ba is not easy all this dayake yi da Waleed maybe kawai dan ya aureni ne danni bantaba ganin wanda yaso yaron dabashi ya haifa ba, ga Momma nan dudda yayar mahaifina ce amman bata kaunata sabida ba ita ta tahaifeni ba, ita kenan yar uwanmu na jini balle wani, Mama yara irinsu Waleed nada gundura, Waleed is selective wajen cin abinci kina ganin zai jure nonsense dinnan, Mama yafara dukansafa? Yafara kyaransa fa? Mama bazan iya jure any form of cutarwa ko takura ma Waleed ba, babu abinda bana tunani yau dinnan, kawai I’m scared ne” tafashe da kuka sosai Mama na shafa bayanta tai murmushi tace “kodan abinda kika mana Safeerah bazaki taba tabewa ba, i know badan kanki kika yarda da auren nan ba saidan mu, banda haka Salim seems like a good person, yanada hankali, gashi yanada natsuwa, wlh hakanan inaji ajikina bazai taba cutar da Waleed ba, idanma yayi muna raye fa zaki maido mana dashi daman ba kowa ke iya rike danda banasa ba” rushewa da kuka tayi tace “Mama ni wlh duk auren dazanyi da Waleed bazai zauna dani ba saidai auren yamutu, ni bazan rabu da Waleed ba” kawai tasama Mama kuka Mama tadanyi dariya ta jijigata tace “toh mara kunya naji mai d’a zan tayaki da addu’a, Allah ya sanya albarka a auren nan, yabaku zaman lpy kinji, Allah bazai wulakanta ki ba Feerah, share fuskanki kibude abinda yakawo miki” gyadama Mama kai tayi tadago takai hannu tana goge fuskanta tass sannan tadauki jakan tabude ahankali waya tafara cirowa iphone 16 pink, saikuma bandir na yan 1k guda 30 sababbi that’s 3million, ahankali ta kalli Mama, Mama ma takalleta saikuma tace “kudin maybe shirye shirye ne na abubuwan dazakiyi, zan dauk some of the money shima sabida matar dana sani a

chan GRA dake zuwa yima yan unguwan gyaran jiki ne, yarinyar tacemin Mamanta na yin na amare yanakai 1m zamu biyata sai amiki gyaran jiki mai kyau sosai, nima kuma zan miki nawa, gobe zanje kasuwa na sayo duk wani abu danake bukata karki wasa da shan magunguna kinji yar kirki" turoma Mama baki tayi she knows menene kayan mata sarai kawai bataga amfanin sha bane.

Sabida Layla yaje gidan yayi dropping nata dan she comes for wedding nasa sai bayan bikinsa zata koma gidanta, Ammi da Dad dukansu fushi suke da shi babu wani wanda ke kulasa cikinsu, sunsan anyi auren dan Baffa yakawomusu sweet da goro but babu wanda yace mai wani abu cikinsu saima fita dasukayi daga harkansa fitowa yayi daga gidan kawai yawuce barrack.

Dayake yau ake fara event, yau kauyawa day akayi ansha shagali agidansu, all he knows is yana bata everything datake bukata saidai in bata gayamasa ba but he won't participate shi baison parties ma so bazaije ba, ahankali yake driving kansa wuraren 9 cikin estate nasu dake da kyau, parents din Nanah are rich but not kaman su, Mahaifinta is a very good friend of Dad, horn yayi gidan gateman na ganinsa yabude gate da gudu yana dagamai hannu. "Sannu da zuwa Alhaji" dan dakatawa yayi yaciro kudi masu yawa yabasa gateman din harda tsalle yace "godiya nake Ogana Allah taimaka" wucewa ciki yayi yay parking yana kallon gidan acike da chairs masu shara haka na picking robobi da trash dai na event da akayi, wayansa yaciro yafito da number Nana she has been calling him fo[4/14, 8:08 PM] AMINA KABIR CAP: □LOKACI BAI KURE BA□

✍M SHAKUR

SUBSCRIBE PLEASE □

SOMETHING BIG IS COMING □□

https://www.youtube.com/@mshakur

EPISODE 32

sauka akan wani bangare na jikinsa, hannunta is so soft and warm, ture hannunsa tayi da muryan da bata fita fa kyau tace "karka dakeni dan Allah Abbati, kayakuri Innalillahi..." surutai tafara da at a point baya ganewa sai kawai yakai hannuwansa biyu bayanta yasata a kirjinsa da kyau yawani matseta yana daura bakinsa saman kanta dake kamshi sosai yace "shillii it's okay babu wanda zai dakeki! Shiiiii" ahankali tasoma rage surutan datakeyi saitai shiru tareda manna kanta ajikinsa shima sai yayi shiru having wani kalan feeling of peace da natsuwa da bai taba jin kalansa ba tunda Allah ya halitto sa a duniya, motsin datayi yasa ya zare hannyensa daga bayanta yana zare fuskansa daga saman kanta, bude idanunta rass Safeerah tayi jinta a kirji mai bala'in taushi da kanshi yasa adaburce tafito daga jikinsa tana komawa baya tama kasa kallonsa sai hannayenta data aura saman kanta ganin bataji gyalenta ba yasa tajuya mai baya tana neman gyalen, gashinta yabi da kallo kasa daurewa yayi yamika hannu yataba jelan gashinta dasauri tajuyo hakan yasa yacire hannunsa jin gashinta ne, tadaura gyalen saman kanta, ahankali tace "I'm sorry bazan kara ba" cikeda isa yace "good! The next time kika sabama dokata you will be punished" dan kallonsa tayi aranta tace "wani irin miji kaddara yasa naje na aura? Ko tausayina baijiba na suma" a reality ta gyadamai kai batai magana ba, dan sassauta murya yayi yace

"wacece ke tare da Waleed?" Anatse tace "my cousin Yasmeen yarinyar Ummi dakai magana da ita" baisake cewa komi ba yace "kawomin credentials dinki" gyadamai kai tayi tabude kofa ahankali tafito ta maida kofan tarufe duk yanda yaso yadaure kasawa yayi hakan yasa yabita da kallo sai yaji abun nakara bata masa rai yanda tafito ahaka yadena kallonta, files na credentials dinta tadauka har tafito daga durin nata sai ta sami kanta da komawa tadauki maroon hijab dake kan sallaya ta warware tasaka tafito, yana zaune cikin mota yaga tabude kofa ganinta sanye da hijab saiya sami kansa da tsareta da wasu mayun idanu hakanan zuciyansa tamai dadi sosai kusan ta goge duk wani haushi dayaji earlier dawowa tayi tabude motan da sallama tashigo tamikamai karba yayi yace "okay zaki iya tafiya" gyadamai kai tayi sai chan da murya chan kasa tace "naje na nemo su Waleed?" Jin yamata shiru yasa tadan kalleshi ahankali tace "Yasmeen batasan ko'ina ba a Katsina take zama tazo hutu ne maybe bata gane gidan bane saisa basu dawo ba har yanzu" batare daya kalleta ba yace "koma ciki i will look for them" gyadamai kai tayi tafito ahankali tamaida kofan tarufe tawuce tashiga ciki yatada motan yayi kasan layin hanyar dayaga sunbi yabi hango playground na yara yasa kawai yayi wajen Yasmeen yagani tsaye Waleed na wasa sosai tana mai clapring, murmushi yayi kadan yana kallon Waleea wlh he loves the boy har ransa, parking yayi yabude mota yafito yazagayo Waleed na cikin wasa kaman ance yadago kansa yaga Salim dawani irin sauri yataho da gudu bai damu da kasan dake jikinsa ba Salim yabude masa hannu Waleed yazo da gudu kawai yadaga sa sama yace "Assalamu Alaykum Champion Waleed" Waleed yace "w'kumu salam" murmushi yamai Yasmeen takallesu ganin Waleed ya sansa yasa tace "ina yini" gyadamata kai yayi batare daya bata second look ba yace "muje gida" bude gaba yayi yasa Waleed yarufe kofa yazagayo ya shiga mazaunin driver hakan yasa Yasmeen tadan taho tabude

baya cikeda fargaba tashiga ta zauna, Salim yaja motan Waleed na wasa a kujeran har gidan parking yayi Yasmeen tace "muje gida Waleed" make mata kafada yayi, batare daya kalli Yasmeen ba Salim yace

"shiga ciki zan dawo dashi" batai musu ba tace toh tasauka yatada motan yabar wajen, shopping yayoma Waleed sosai harda kayan wasa sannan yadawo dashi yakira Safeerah awaya yace "fito" fitowa tayi shima yafito dauke da Waleed yace "Waleed go to Mom" dasauri Waleed yamikamata ball dinsa yace "Ummyyy see" murmushi Safeerah tayi tace "laaaa Abee yasai maka"? Dan kallon Safeerah Salim yayi itama saida tai maganan taji wani irin kunya saitaga kaman tana chusa masa yaron da ba nasaba, Salim kuma har cikin ransa yaji dadin sunan datake koyama danta yakirasa dashi, karban Waleed tayi batare data bari sun hada ido ba tace "angode" tajuya tawuce ciki baya yabude yaciro ledan yazo wajen kofa ya ijiye yawuce mota yamata text akwai kaya yawuce mota yamata text akwai kaya gaban kofa sannan yatada motansa yabar wajen, saida sukaji tafiyansa Yasmeen tace "ke wannan hadadden mutumin ne mijinki? Kinga yanda yakeson Waleed kuwa kai amman wh baida kirki, baiso na shiga gaba yasa Waleed awajen ya aikani baya" maganan ba karamin dariya yaba Safeerah ba tace "Alhamdulah na dauka ni kadai na ke ganin baida mutunci kema kin gani Yasmeen, saisa bana sonsa kawai sabida su Baba ne Allah ma yasani, amman ni I hate men, I hate aure!" daidai text dinsa na shigowa, ahankali tamike Yasmeen tace "ina zaki"? Batai magana ba tabude kofa taga katuwan leda saitai gmmm hakan yasa Yasmeen tazo wajen tasa hannu tadauka tace

"Waleed zokaga toys naka" da sauri Waleed yazo wajenta suka zauna anan falo suna fito da komi Safeerah tamaida kofa ahankali tarufe tadawo kawai ta zauna tai shiru tana kallonsu barinma yanda Waleed ke murna toh he has not been getting toys ga snacks dayawa daban daban na yara, Parking mota sukaji anyi dasauri Yasmeen ta tashi tai window ganin su Mamanta da Momma harda Salma yasa tajuyo cikin whispering tace "ke harda matar nan da yarta" daidai nan Baba yayi sallama yashigo Mama biye da shi sai Mom, sai Momma da alma

dasukabi ko'ina na gidan da kallo idanun Salma na sauka kan iPhone 16 data gani a hannun Safeerah taji wani abu a wuyanta, yaushe su Baba da Mama suka fita daga gidan nan? Tasan suna nan fa dazu, suna hada idanu da Momma Safeerah ta sauke kanta kasa tajuya ahankali tace "ina yini Momma" "lafiya kalau" murmushi Zainabu tayi duk aka zazzauna Safeerah ta wuce zatai hanyar stairs Baba yace "zo Mamana" juyowa Safeerah tayi ta kalli Baba ita suke boyema abu, Salma takalli Waleed tace "zo Waleed dina" makemata kafada Waleed yayi ya manne jikin Mama yadena wasan ma dan sarai yaganesu, Momma dake kallonsa tace "harka manta mu rigimamme" fitowa Yasmeen tayi da drinks da snacks, Baba yakalli Safeerah yace

"badake nake magana ba Mamana" Zainabu tace "zauna Safeerah" zuwa Safeerah tayi ta zauna ahankali kanta akasa.

Anatse Zainabu Mom tace "nasan abubuwa da dama sun far but yanzu ba lokacin maimaita kace nace bane, mu ukun nan iyayen mu suka haifa, zumunci yawuce wasa, komunaso ko

bamuso duk jini daya muke anan, komi yariga yawuce, Momma mahaifiyarki ce Safeerah ke kuma diyarta ce, an samu sabani ada kwarai but yafiya yazama dole dan haka inaso kibata hakuri sabida arufe chapter gabaki daya abude sabuwa afara shirye shiryen biki" Zainabu tal shiru duk ana kallon Safeerah data haderai sosai takalli Zainabu tace "ni bazan bata hakuri ba sai yarta Salma tabama Babana da Mamana hakuri! Ai iyaye basufi iyayeba, bakuma daraja tafini ko iko ba dazatai tunanin zata zagi iyayena ta gayamusu maganan banza k zata bada hakuri ba sabida sunada kudi mu bamuda shi dan haka ni nabayar, I am never going to live wannan rayuwan again, I am sorry Ummi but zumunci ba dole bane, and idan kunaso ayita daga yarta har ita Momma saisun bama iyayena hakuri ko sutashi su bar gidan nan!" Kowa na dakin kallon Safeerah yake Safeerah ta bala'in burge Yasmeen, Baba yace "Mamana kinkosan Momma Adda na ce?" Ran Safeerah abace tace "Baba nikuma yarka ce!" Mama ko kadan bataji zafin maganganun Safeerah ba, Ummi takalli Salma data batarai tace "sauka kasa ki duka kiba Baba da Mama hakuri dan kin musu ba daidaiba" saukowa Salma tayi

Safeerah na kallonta sosai tai murmushi tace

"Baba and Mama nayi kuskuren abubuwan dana muku kuyakuri kuyafemin, bazan karaba, I am very sorry about everything" saikuma tajuyo takalli Safeerah ahankali tace "I am very sorry cousin forgive me okay" kasa yarda Sa erah tayi Salma Salma dai data sani ke bada hakuri haka, Baba yace "mun yafe miki Salma, Allah ya yafe mana gabaki daya" yakalli Safeerah yace

"Adda na don't have to tell me sorry agabanki, tana gaba dani kuma daga gidanta muke now kibata hakuri Safeerah ko zan sabamiki" hawaye cikowa idanunta sukayi ahankali tace "kiyakuri Momma kiyafemin" murmushi Momma tayi wanda iya lebe ya tsaya tace "bakomi yawuce

Allah ya yafemu gabaki daya, ga yar uwanki nan Salma sai ayi komi tareda ita, ga Yasmeen itama tazo kuhada kanku kunji, let us all close the old chapter" gyadamata kai sukayi, Momma ta kalli Salma tace "Feerah batace tayafe miki ba sake bata hakuri" ga mamakin Safeerah sai Salma ta taso tana murmushi tazo gabanta sai kawai ta rungumeta tace "I'm sorry Feerah! And I love you so very much, sorryyyy pleaseeeeee, I am ur big Sis fada dake is norms but baran karaba kiyakuri kinji, I love u alot"wani sanyi Safeerah taji idanunta suka cicciko da hawaye tana tuna abubuwa da dama da Salma t nata takai hannu ta goge hawayen dasauri Salma ta taso takalli fuskanta takai hannunta ta share mata a fuska tace "I made my sister cry kiyakuri Kinji forgive me pls" muryan Safeerah nadan rawa tace "yawuce nima kiyakuri duk abinda namiki" Salma tace "yawuce har raina" takara hugging Safeerah tana shakan kamshin datake da ita kanta mace tanaji kaman ta hadiye

Safeerah balle kuma namiji sannan tasaketa tace "Yasmeen kutashi muje sama dakinmu mubar iyaye suyi magana" Salma tasa hannu tawani kama Safeerah tana dagota sukai sama while su Baba suka cigaba da tattaunawa.

Sosai Salma tadinga hira dasu tun Saicerah bata sakin jiki harta saki jikinta suna hira dan gaskiya batada riko ko bakin zuciya, idan ta yafe ta yafe.

Sai yamma Momma tace tazo sutafi Salma tace ita anan zata kwana, Yasmeen daman tana nan haka ma Mom ga mai gyaran Safeerah, Salma so kawai tasan wanene me kudin daya chanza rayuwan mutanen nan haka? Who is he?.

[4/19, 10:43 AM] AMINA KABIR CAP: EPISODE 43

Around 6 na yamma ya sauka a lagos jirgin yan airforce yabi, wani gidansa dake Ikoyi yaje, shifa daman yanada yawan tafiye tafiye but wannan is work related, kawai he just wants to rest from all the bacinrai na this past few days sannan yayi prepping kansa for this walima and tarewan matarsa. Gidansu yacika dayawa ga gidansa na barrack ana aiki, duka duka yau is just 3days left a daura auren Auwal da Nanah, he just pray kanninsa enjoy this marriage and he wish them the best, May Allah bless union nasu, bazaije daurin auren ba cus baimaso yahadu da family ta at all yariga yabarta yabarta baiso kananun magana. While tarewan Safeerah saura 10days yau, sai ana 3days to tarewanta zai koma Abuja.

Wanka yayi yaci abinci cus yanada chef yakirasa kafin yazo daman yayi shiru he's just remembering the hug he shared da Safeerah, how he felt in his body baitaba jin hakaba, yakasa mancewa cus it's such a great moment for him, this days kuma bacci na gagaransa all because of the hug, what is happening to him?

What is wrong with him? Shi yasan har cikin ransa, harga Allah sabida ya taimaki Safeerah ya aureta, he deeply cares for her sabida she deeply cared for him then, she was crying for him sosai seeing him in pain mutamun dabata saniba just because tagansa in pain, is that the reason yake jinta haka in his mind har bayaso yahadata da wata? He knows this Safeerah is one big reason dayasa he couldn't go on da auren Nanah, he just wanna see her smile, and happy, idan yaga she is sad he feels sad, yanzu he thinks he feels something else especially when she hugged him, and he keeps feeling the urge to go back for the hug maybe yamayi advancing, kiss, also love making, sake lumshe idanu yayi tsigan jikinsa natashi abun is too much kaman zai haukace sabida ita, kaman yakira yasa akawomai ita Lagos right now, sai kawai yakai hannunsa yadauki wayansa yay! dialing number ta, Yasmeen tafita ta zubo musu abinci, Safeerah na bayi, while Salma na kan gado har yanzu batai isha'i ba su duk sunyi ganin wayan Safeerah na ringing taga Major Salim dasauri tadauka takai wayan kunnenta tawani kashe murya kaman yar mage

tace "Hi Major Salim" danzare wayan yayi daga kunnensa ya kalli screen sannan yamaida wayan kunnensa kawai ransa yahau baci da kyar kaman ana begging dinsa yayi magana yace "where's my wife"? Yayi maganan cikeda iko, sounding brutally rude cikeda rashin mutunci fa, wani iri Salma taji jin baida kirki irin he's not even interested in knowing waye ita data dauki wayan ko? Matarsa yake tambaya baida ma interest na sannin wacece ita ta dai daure cike

da duniyan ci ta sake kashe murya tace "I am Salma Feerah's Cousin, she's using the restr..... dip ya katse wayan daidai Safeerah nafitowa daga bayi dasauri Salma taji gyara fuskanta tajuyo tana murmushi tamika mata wayan tace

"wai wannan miji naki kaman mai anger issue baima jira na gama gaya masa kina restroom ba, wai Allah sa dai ba mai dirkanki kika kwaso ba, dan masu kudin nan sai ahankali barinma sojoji Allah sa ba yayan Abbati bane wannan ba" daidai Yasmeen na shigowa dakin tace

"Allah yarabata da mutane irin su Abbati kekuwa Salma kidinga fadin alkhairi, not all men are bad" dasauri Salma dataji kaman ta make Yasmeen tace "ke kinsan waye Soja kuwa? Me kika sani game da Soja? Lemme tell you kadan, kinga Sojoji akwai su da son mata, ga iya dukan matan kuma, ga hanasu fita wlh, ga balain neman mata, mace daya bata isarsu that is masu tsoron Allah kenan da basabin na waje, ga uban kulle, basa barin matansu da kawaye, ga kishi ga kishi maida matayensu ustazai suke wasu har nikabi sukesa matansu sawa, sannan basu da kirki ga bakin mugunta" wucewa abinta Safeerah tayi tai kaman bata jinsu but gabaki daya duk maganan na kunnenta, somehow she's believes

Salma cus zancen kulle da all those rules tagani, da sauransu, gabanta se faduwa yake, anytime zatai tunanin wani abu she remembers she's doing it for iyayenta da ba auren nan ba da yanzu suna gidan Momma an cigaba da wulakanta su inama ace zata sami wani aiki ko kwangila da zata sami kudi tasayama iyayenta gida dataji dadi wlh, kayan bacci tasaka tadawo ta zauna cikinsu zatai magana wayanta yafara kuka Yasmeen tace "yana kira again kai wannan miji naki na sonki Feerah" daukan wayan tayi ahankali saita tashi daga wajen tazauna kan gado takai wayan kunnenta tana dan satan kallon su Yasmeen da Salma daba ita suke kallo ba tace "hello" batare daya amsaba yace "next time tell those people su dena daga miki kira"ahankali tace "tom" sukai shiru kirjinta nadan bugawa gently tace "ina yini" ahankali yace

"how are you? Ya Waleed?" Batasan mesa ba anytime ya tambayi Waleed wani irin sanyi takeji aranta mara misultuwa tanason aso Waleed, duk maison Waleed automatically yake stealing heart nata, ahankali tace "Alhamdulillah we're fine, Waleed na wajen Baba akasa" gyadamata kai yayi chan yace "nayi tafiya ina Lagos" shiru tayi batasan mezatace ba, ahankali yace

"ana biki agidan mu, Auwal is getting married rannan asabar" asanyaye tace "Allah sanya Alkhairi, Allah yabasu zaman Ipy"shiru yayi yana sauraron addu'anta harta

gama zuciyansa namai dadi sosai, murmushin yayi kadan da saida taji karan murmushi hakan ya mugun bata mamaki dan bata taba gani ko ji yayi murmushi ba sai yau, ahankali yace "Ameen nagode, kina bukatan wani abu"? dan shiru tayi kafin tace

"a'ah" takasa sakin jiki dashi batamasan tayaya zatayi ba, even though ta taimakesa da to ko

aranan ai duka duka awa nawa sukai tare and she was small then ga yarinta, batasan ya ake mu'amala da maza ba, yanaso yajata da hira taga he is not that strict or wicked datake tunani but he noticed bata iyaba, hakanan even though bawai wani maganan kirki takemai ba tana dari dari dashi but he's enjoying dan maganan dasukayi, kaman karya mata sallama but baisan mezai kara cewa ba jin shirun yayi yawa yasa yace "saida safe" "Allah tashemu Ipy" Safeerah tafada dasauri ta katse wayan ta ijiye wayan ta sauko kasa suka cigaba da hira.

Yana gama wayan Sister sa yakira Layla cus bayason yana damun Anty Asbae ringing daya ta daga tace "ina yini Yaya" batare daya amsa ba yace "kungama hada akwatin?" Dasauri tace

"laaaa Yaya jiya fa kabamu kudin"..

Waleed adakin Mama ya kwana sabida baida wuri adakin Safeerah, kasa bacci Salma tayi kaman an samata dutse a kirjinta sai juye juye take, how can this stupid poor girl be this lucky? Tashi tayi zaune ahankali daman Yasmeen na minshari itakuma Safeerah ko da chan tanada bacci dawuri and tanada nauyin bacci ko motsi bataji, around 2:30 ta tabbatar bacci ya shigesu sosai ta tashi zaune takai hannu saman cupboard tadauki wayanta tareda wayan Safeerah data lura tun dazu kaman ba password, call log nata tashiga tadauki number Major Salim tasaka a wayanta tai saving da Xoxo sannan ta shiga neman WhatsApp a wayan taga babu Safeerah batai installing wani app a wayan ba, basuyi sharing text messages ba kawai waya suke taso tadan karanta chats nasu takara fahimtan waye Salim but batasami komiba, tsaki tayi ta maida wayoyyin ta ijiye ta koma ta kwanta, tayaya ita ko saurayi guda tsayaye batada shi sai talakan yarinyar nan eh? Tana diyar governor amman diyar makaho tafita zama lucky arayuwa is not possible! She will plan something big da saiya saketa wallahi kuwa kuma she will steal Salim from Safeerah alkawarin Allah.

[4/19, 10:43 AM] AMINA KABIR CAP: EPISODE 44

Wasa wasa agidansu Nana sai event ake daban daban, Mommy is very angry with Nanah da Abba cus takirasa ta masa maganan but shima idanunsa yarufe wai a ina yarsa zata taba samin family that loves her haka, karta karamai maganan, kawai ta

zubamus ido, Nanah ta warware kaman ba ita ba she is so happy kuma Maman sai kallonta take taking pity on the girl.

Nana is smart duk wani abu na bikin is sunanta da Salim, da gangan tasaka friends nata sukai snapping komi aka watsa a duniya harda biyan blogs su dauka sabida tanason koma wacece matar nan daya aura inhar she is on the internet taji labarin bikin Major Salim da Nana.

Yau Salma na gidansu, one thing about Salma tanada all those rich girls as friends, tana WhatsApp dube duben status taga wata friend nata dasuke kira da Maska tasaka status da hoton Nana saikuma hoton Major Salim da uniform na sojoji even though kana ganin hoton kasan photo shop ne but dawani irin sauri Salma ta tashi zaune this is mutumin datake suspecting shine mijin Safeerah ta gansa rannan yadauki Baba, kuma mijin Safeerah name is Major Salim, wani shewa tayi. "Ahayyeee menake gani haka? Maska ba wannan ne Major Salim na Safeerah ba did I see he is getting married tommorow asabar" jikinta har rawa yake tama kawarta voice note tace "Maska suwaye this cute couples?" But Maska bata online Instagram ta shiga haba saiga vlog sun dauki komi, harda backdrop na wajen event dake dauke da hotunan Salim da Nana da akayi, dudda Salma na son Salim but wani dadi dataji batasan sanda tahau rawa ba tace "Safeerah kenan jibi buzuwan dayake aure, budurwa, yar controller general, ajebota girl tayi school a UK wayyooo Momma" tawuce dakin Momma tabata labari tasss kunga yanda sukajin dadi Momma tace "shirya jeki nuna mata mijin dasuka samu aketa mana tunkaho, sorry for her batasan waye yaran masu kudi ba" tashi Nana tayi ko wanka batayiba sai gidansu Safeerah, parking tayi awaje tashigo su Baba ta gaida ta wuce sama Safeerah na daki tana shigowa takama kirji tace "Safeerah daman aure mijin naki zaiyi budurwa zai aura buzuwa yar controller, kinga yanda bikinsu ke trending a social media?" Dan kallonta Safeerah tayi batama gane kan maganan ba, dasauri Salma ta zauna tashiga nuna musu komi da komi ita da Yasmeen na kallo, Salma tace "bikin na trending a social media sosai yaron richest man finally is getting married" harga Allah tasan bata sonsa tasan ba auren soyayya suke ba but dataga matarsa Nanah saitaji ta raina kanta yarinya kaman balarabiya sabida haske, ga kyau gashi taga suna son juna hotunan su yawanci suna kallon juna, wani abu taji ya tsayamata a wuya, Salma tace "budurwa kuma ce bata taba aure ba, bana gayamuku sojoji nada aure aure ba"

daurewa Safeerah tayi tace "Allah basu zaman Ipy, bari naje nadauko Waleed namai wanka" tawuce fuuu tafita Yasmeen ta kalli Salma tace

"mesa kika nuna mata this?" Hararanta Salma tayi tace "I know bai fada mata zaiyi aure ba akanme na gani ina yar uwanta bazan gayamata ba" tashi Yasmeen tayi kawai tafice tabita, tun lokacin har zuwa dare Safeerah bata saki ba mai mata gyaran jiki da Mama saida suka tambaya tace kanta ke ciwo, Salma sai wani dariyan dadi take tana gayama Yasmeen bata cemusu sojoji mayun mata bane, suna nan zasuga ya auro wife number 3 barinma wannan da yanada kudi, yakira Safeerah

sau biyu bata dagaba kawai haushinsa takeji, sake kiran wayan yayi da daddare har saida Yasmeen dake bacci ta farka ta tashi zaune da sauri taga Safeerah azaune but ko wayan bata kallo, takalli screen din sannan tadafata tace "Safeerah ana kiranki" dan kallonta tayi gani tayi idanunta sunyi ja ahankali tace "bar wayan Yasmeen nayi bacci" ta ijiye wayan zata mike Yasmeen tarike mata hannu kawai saiga hawaye dasauri Yasmeen ta tashi tace "menene Safeerah"? Rungume Yasmeen tayi tana kuka sosai jikinta na shaking ga hawaye tace "wih nadaman auren sa nake, Allah kuwan Yasmeen da akwai inda zansa su Baba dana basa takardun gidansa nace ya sakeni, I hate aure wlh, I hate maza gabaki daya, na tsani auren nan" bayanta Yasmeen ta shiga shafawa tace "shiiili ya isa Safeerah, it's okay, zoki zauna, I know wat u are feeling" zama tayi tace "I'm not feeling anything wallahi dama ba sonsa nake ba, kawai dai he looks like wanda bai dauki y'a mace da aure a bakin komiba, he has the money toh, ni mema yakaini na yarda? Da mun hakura da zaman gidan Momma haka nan duk bakin halina yasani in this situation" dasauri Yasmeen tace "sabida Momma takarasa kashe Baba, ke are you not happy kiga Baba yanzu healthy yana ganin komi da kowa" shiru Safeerah tayi sai share fuska take da bayan hannu tana shesheka ta bala’in bama kanta tausayi, Yasmeen taji kuka yazo mata amman tadaure tarike hannuwanta tace

"Safeerah I don't want you to loose hope, think, ko da bai aure ki ba rayuwa ahaka daman ba miji bazai yu ba, think of Waleed, su Momma were not ready su cigaba da ciyar dashi daya zakiyi toh eh? Even if not for anything for the sake of mutumin nan nason Waleed and hes taking care of the boy ai ya chanchanci aurenki, kiyi zaman auren nan for Waleed sabida yasami kulawa ya girma yazama wani abu, kinji forget Salim din da matarsa and live your truth, kina gidansa sabida you want iyayenki and danki well kept kuma ai bai miki komi ba as long as I know" gyadamata kai Safeerah tayi takai hannu ta share fuskanta tace "naji Allah baya bacci bakomi i will not cry again" Ganin yana sake kira yasa Yasmeen tace "ki dauka" bayan hannu takai ta share fuskanta tass sannan tasa hannu tadauki wayan takai kunnenta ahankall tace

"hello" shiru yayi na kusan 5secs kafin ahankali yace "meya sameki kike kuka"? Ita tambayan ma tsoro yabata to some extend hakan yasa murya ciki ciki tace "kuka kuma? A'a ni ba kuka nak...."

"why did you cry Safeerah?" Yayi tambayan kai tsaye da dan zafi sai taji kaman tambayan ya soso mata kuka again tai shiru tana hana kanta kuka dan tana bude baki kukan zai fito, Yasmeen na girgiza mata kai alamun kartayi, runtse idanu tayi takasa magana, daga ta dayan bangaren asanyaye yace "Safeerah!" Har kasan zuciyanta taji yanda yakirata hakan yasa calmly tana nokewa tace "kaina ke ciwo" alamun motsi taji yace "bari nazo na kaiki hospital" dasauri tace "nasha magani basai ka zo ba kaida ke Lagos, bacci nakeji sosai" dan dakatawa yayi ya tsaya yayi shiru hamma tayi tace "bari nai bacci" bata jira amsan sa ba ta katse wayan dasauri tana kashe wayan gabaki daya switch off ta ijiye wayan a gefen gado ta kwanta Yasmeen ta hayo gadon kawai ta rungumeta tabaya tace

"everything will be fine Safeerah kinji rayuwa yagaji haka, gwara dabaki fadamai komiba hankalinsa yatashi gobe aurensa" kankame hannayen Yasmeen Safeerah tayi tace "I just wanna do well on my own wih banson auren, I hate marraige, I hate aurensa shima I hate him sosai, wih kaman nace na fasa kawai banda inda zansa su Mama ne, Yasmeen na tsani komi nakeji" kanta Yasmeen ta daura gefen fuskanta tace "stop saying all of this sabida ba solution bane, bakiga yanda Momma ke girmama Baba yanzu ba sabida yayi gidan kansa, no condition will ever make you go back to gidan nan da izinin Allah, please calm down"

Baki Yasmeen tadinga bata ahaka bacci yayi awon gaba da ita Yasmeen tai shiru tana kallonta kafin takoma ta kwanta taja bargo itama tai bacci.

Da asuba suka tashi Alhamdulillah ta tashi Ipy duk wannan zafin zuciyan da damuwan yafita aranta gabaki daya she woke up happy ma, kitchen tawuce dan yima kowa breakfast kafin mai gyara tazo, Yasmeen itama bata tashi ba, su Mama tasan sun tashi amman basu fito ba, kitchen tawuce tafara sa abinci a wuta takoma tana yanka dankali ba dankwali akanta gabaki daya batai parking gashinta ba kwana nan haka take barinsa a sake sabida turarata da akeyi, wata simple gown ne ajikinta irin na Egypt gowns dinnan masu manyan mayafi but bata sa mayafin ba, ba bra ajikinta, boobs dinta are standing suna wani dangling zaka rantse yaro bai sha ba dan gaskiya Waleed bai sha sosai ba dayake tayi ciwon nono bayan ta haifesa daganan yaki nono, yaki sha daga jikinta saidai ta matse a bottle shima daga baya yadena saidai yasha su madara, saisa yataso dasu son

abincin turawa.

Daidai tazuba Irish a wuta taji an danna doorbell nasu fitowa tayi ahankali daga kitchen din wutan falon su ko kunnawa ba'ayi ba cus is very early around 6 waye haka ko Zainabu ce? Ko Umma mai gyara but ai around 8 take zuwa not around 6 haka? Bawai sunada wani Neigbour masu zuwa wajensu bane waye this early morning, kai tsaye ta murza key tajawo kofan tabude atare gabansu yawani mahaukacin fadi dummmm! Salim tagani yana sanye da jean blue da faran t-shirt kafansa sanye da trainers yayi zufa a goshi ga zufa a rigansa kaman he ran here dan ba mota awaje kawai ya tsareta da ido, tundaga kan kafarta dake cikin farinslippers yake kallo, kumbunanta farare fess dogaye, zuwa jikinta, da gashinta dayake a sake bakin kirin har wajen waist nata, idanunta sunyi fari kal but sundan tasa alamun tai kuka, ga lips nata so pinkish sun bushe, wani kalan racing zuciyansa yashigayi ganinta baisan meya samesa ba samun kansa yayi da dawo da idanunsa daga fuskanta dayake kallo zuwa kirjinta kaman anyi fixing idanunsa awajen abun was so crazy and new for him yanasa kansa yacire idanu daga wajen yakasa har saida Safeerah ta lura awani irin rude tajuyamai baya dasauri tuna babu komi ajikinta zata wuce dawani irin sauri yayi one step yashigo falon yakai hannunsa yawani fizgota tajuyo kaman paper jikake kum tafado cikin kirjinsa yanajin saukan boobs yakai hannu daya yana tura kofan yarufe, boobs dinta kan kirjinsa da balain sauri Safeerah tai baya zata fita daga jikinsa hannunsa yakai bayanta yaturata back

cikin kirjinsa boobs nata gabaki daya na mannuwa da kirjinsa yana matso da fuskansa dab da nata yana shakan kamshin datakeyi da yahau kwance masa lissafi yana kallon lips nata dake rawa sosai yace "did you know abinda kika min jiya" batare data dago idanu takalli fuskanshi ba feeling very uncomfortable gabanta kaman zai tsage tace

"Ba....Baba da Mama zasu fito, dan Allah ka sakeni" yana kallonta sosai yace "anki, saikin fadi dalilin dayasa kika kashemin waya, did you know what i went through to come to Abuja this early morning sabida ke? Speak Safeerah" kasa dago kanta tayi gabanta na faduwa wani bala'i ta tsokano gashi wani irin riko yamata ko motsi bata iyayi Innalillahi kaman machine ne yariketa, yamata mugun mahaukacin kwarjini bamata iya kallonsa tana gab data fashe da kuka, strictly yace "bakiji nace ki magana ba" gabanta na faduwa sosai muryanta na breaking tana kallon side danta kasa kallonsa tace "wa.....wa...yan mutuwa yayi na mance bansa cha.....ji ba" yana kallon fuskanta da facial expression nata da yanda take magana bayako kyafta idanu yana shakan scent na breath nata dudda safiya ne ba wari ko kadan she has wani irin calm children breath smell that he loves just like that, is kind of sexy for him, and she smells incredibly magical, sake matso da fuskansa yayi dab da nata hakan yasa tashiga komar da fuskanta baya hannunsa daya yazare daga bayanta yakai keyanta yatare yawani turo fuskanta back har saida yahada fuskansa da nata wani irin nishi Safeerah tafara kaman zata shire sabida tsoro kawai ta kulle idanunta gam hawaye suna gangarowa suna fitowa ahaka, ahankali yace "yaushe kika fara karya?" Lips dinta motsi suka shigayi suna rawa tama kasa magana takasa bude idanu fuskansa na dab da nata fa, rage murya yayi sosai yace

"why did you cry yesterday"? Wih birkicewa tayi gashi yariketa gam gar yanzu kirjinta manne da nasa, hannunsa abayan keyanta he's in control of every part of jikinta, fashewa da kuka tayi but ba kara sosai kar ajiyosu tace "dan Allah ka barni nasa Irish a wuta" yana mata wani mayen kallo muryansa sounding really sweet and charming yace "fadi gaskiya toh Pretty girl" dasauri tabude manyan idanunta dake jike da hawaye for the first time ta kallesa, hada idanu sukayi saitaga idanunsa sundan kankance sunyi ja kaman zaiyi bacci yasaki fuskansa sosai ga signs na alamun kaman murmushi zaiyi yana kallonta bata taba ganin fuskansa so close haka ba and so asake haka, yana kallonta still sounding very sweet kaman yana lalashinta yace "do you want a kiss before ki gayamin meya samin ke kuka jiya"? Tsabagen tsoro da yanda gabanta yafadi batasan sanda ta damke bakinta ba ta harde lips nata gam, dan murmushi Salim yayi Safeerah tazaro idanu sosai tana kallonsa ganin murmushi kan fuskansa, calmly yace "speak Madam Salim" jin ana bude kofa a sama yasa ta birkice tai raurau da idanu ta kallesa hade fuska yayi ko ajikinsa baima da niyyan sakinta, rasa yanda zatayi yasa cikin yar kankanuwan murya tace "I felt bad na shiga tsakanin ka da Matar ka, I'm regretting aurenka wih, dama banyi ba, naga yaune bikinku, toh shine abinda yasani kuka" tunda take magana yake kallonta somehow he sensed taga hotunan bikin cus an gayamai

bikinsu is trending a social media, calmly yace "mena gayamiki about social media?" Dasauri tace

"Salma ta nunamin a wayanta" tsayawa yayi shiru yana kallonta dasauri ta runtse idanunta ko kadai batai tsammani ba kawai hugging nata taji yayi tsamtsam ajikinsa ya manna hancinsa cikin gashinsa a gefen wuyanta yayi lamo ajikinta yana shafa bayanta kaman karamin yaro jikinta yadauki rawa sosai tanaso ta tureshi takasa sai kallon bene take tama kasa magana, cikin wata murya kaman batasa ba yace "auren dakike regretting kinriga kinyishi and its forever and ever, you're stock with Major Salim Pretty!" Wani sanyi taji jikinta yadauka, murya chan kasa ahankali kuma yace "hawayenki saidai su kare nothing is going to change that! Bye"

[4/19, 10:43 AM] AMINA KABIR CAP: EPISODE 45

Kawai Salim yasaketa yajuya da sauri yabude kofa yafice, sulalewa Safeerah tayi tazauna anan kasa jikinta yawani irin mutu, somehow she feels kaman hug daya mata na lallashi ne amman kuma bakar magana yagayamata a hug din ya maida mata da martanin tai nadaman aurensa data fadi, baice mata anything about bikinsa yauba, abu taji yatokare mata wuya, jikinta duk ya mutu gabaki daya kamshinsa takeyi, duk tai sanyi batasan mesa ba takai 2mins awajen sannan ta tashi da kyar tawuce kitchen nipples dinta sun fito sosai bana wasa ba, dankalin ya konema, kwashewa tayi tasa wani.

Koda yafita ya rufo kofa kasa wucewa yayi saidai ya zauna anan bakin kofa Allah yasama safiya ne babu wanda yafito cus just hugging her and feeling her messed with jikinsa sha'awansa yatashi sosai dudda akwai tight boxer ajikinsa wanda yawanci yan gym da yan kwallo ke sawa sabida yakama gabansu kafin su saka wando but dudda haka yatashi, harde kafafuwansa yayi yana tsaki kadan he hates embarrassing moments haka, wats even wrong with him? As far as yasan kansa is not like he loves Safeerah kawai he deeply cares for her and wants the best for her but mesa zaiji sha'awa takamasa cus he sees her in morning time, muryanta jiya da yanda ya kashe waya ya damesa da he couldn't sleep, he called wani good colleague a airforce shima major ne haka akasa wani pilot nasa yatukosa as early as 5 na asuba daga lagos to Abuja, waya yakira akazo aka daukesa kawai yatafi barrack dan duba progress na gidansa daganan zai kara komawa Lagos.

Wuraren 2 na rana aka daura Auren Auwal Ibrahim Maradi da Nanah Khadijah Maidula akan sadaki Miliyan Goma dudda mutane nata mamaki sunan ya chanza wasu didn't give meaning, wasu feels ina ruwansu, Auwal was feeling somehow, few friends nasa akace ashiga dashi cikin gida for Halal hug, tunda aka fara abubuwan nan bai hadu da Nanah ba itama haka.

Cikin gida aka kaisa zuwa falon Abba inda Nanah ke azaune tana sanye dawasu fararen clothes tayi kyau sosai an mata lullubi, tsayar da Auwal akayi gabanta

yarasa mezaiyi kawayenta sukace hug her, hannunsa har rawa yake yakai hannu ya yaye gyalen dago kanta Nanah tayi ta kallesa she wish Salim nata ne abu taji a wuyanta amman ta daure tai murmushi kadan, aka fara ihu kama hannuwanta yayi yadagota ta taso gently yayi hugging nata batasa hannayenta abayansa ba anata ihu ana hotuna daganan dai suka tafi.

Wuraren 6 akazo aka tafi da Amarya za'ayi event na welcoming Amarya sai sunday zata tare a gidanta, Nanah taga soyayya, tasaki ranta, dudda eyes nata keeps scanning for Salim cikin all the men but basa, washe gari sunday aka kaita gidanta.

**

Yau duka duka tarewan Safeerah saura kwana hudu, gabanta sai faduwa yake she keeps regretting uban abinda yasa tai aure but kuma saita tuna how good Baba is looking now, Salim ya aikama da both Baba and Mama manya manyan akwatina na dinkakkun kaya masu mahaukatan kyau, ya chanzama iyayenta wardrobe, ya ijiye musu 2cars da standard soja cus Baba baigama iya tuki ba dudda yafara koya, kuma Baba ya fara neman koyarwa ma gobe wani school sunce yazo kuma yasoma murmurewa sabida cin abinci mai kyau da gina jiki, Mama ma haka sai kyau take gasu da abinci agida da komi, Salim babu abinda baya kawowa sojojinsa kawai yake turowa dan tun rannan dayazo da safe rabonsa dayazo, jiya yamata text kan su shirya gobe za'a kawo akwati gabanta sai faduwa yake ganin everything is serious, data gayama Mama cewa tayi daman anama bazawara akwati haka takira Ummi da Momma ta sanar dasu itada Yasmeen sukahau aiki sunada komi snack suka kwana that night sunayi, Mama tasa hannu, wuraren 1 suka gama washe gari Mama takira makotanta dasuke dan shiri nan aka hadu ana girki Safeerah da Yasmeen suka fice suka shiga gidan wata Amarya me yaro daya dasuke shiri sanda, Momma da Salma sukazo gayama Salma inda suke akayi tazo tasamesu.

Layla, Anty Asabe da fews kawayenta guda biyu sai Mama Kulu Matar Baffa da Bathoul ne suka kawo akwatunan, wani abu Momma taji ya tsayamata a wuya sanda aketa shigo da akwatunan cus ana expecting akwati yan guda biyu ko daya ma tunda haka akema zaurawa amman saitaga akwati set set guda biyar kowani set nada 7pcs na box, saiga wasu basket na yan gayu suma kayane anyi wrapping anyi decorating aka fara ayiyiriri ana zazzaunawa, kasa hakuri Momma tayi dan gani tayi anya sunsan yarinyar nan bazawara ce kuwa cikeda bakin ciki tai yake tace "bazawara ce diyarmu fa wannan kaya har ina yarinyar harda d'a dan saurayi guda daya Waleed" sauke kanta kasa Mama tayi batace komiba amman maganan yamata wani iri, Ummi tace "mace ko takai shekaru dari mace ce" Umma tace "mu baruwan mu da al'adun nan, munga diya munaso munyi abinda yakamata" makota suka keta guda, aka fara bude akwatina ba su Ummi ba hatta makota dasu Layla saida kowa yaga yanda fuskan Momma ya chanza kunga kayan da akama Safeerah kuwa, Momma ta kirga set set na zinare masu faska faskan sarka guda biyar wanda kudinsu duka zai iyakai 500million ga atampopi babu ta kasa da 200k abaya kusan guda 20 yan millions ne bayan 100k ba, ubanme yakai Shamsu kai Safeerah

kampanin nan data sani da Salma aka kai, Innalillahi jibi arziki this people are rich rich crazy rich, abubuwan aka shiga shigowa dasu sukaci sukai kat sannan suka tafi Mama takawo 300k shima cikin kudin da Salim yaba Safeera tabayar da abubuwan da akayi suka karba sukai godiya sosai da nuna jin dadi babu rainuwa suka tafi for the first time sai Mama taji zuciyanta ya natsu da aure cus sunada mutunci ga karamci kudinsu baisa musu girman kai ba, jibi yanda sukai godiya da kudin mutanen da sunsan sunfi karfin ta.

Neigbours sukama Mama addu'a, Ummi tahada musu komi ta babbasu suka tafi, kaman jira

Momma take tace "aikin banza yarinya zatai aure amman har yau kun kasa sa yaro yazo gida ya gaidani ina head of family dinmu" kallonta

Ummi tayi ta tabe baki tace "maida wukan

Hajiya Kubra Head of Family Salim zaizo ya gaidaki zan sanar da Safeerah ta gayamasa" wani kallo Momma tamata kaman ta maketa tace "wai nazama tsaran wasanki ko kudi yasa kika tarama matarnan biyayya" tanuna Mama data juya abinta Ummi tace "wai me matsala ki eh? Adda me haka? An zauna agidan ki kin addabesu sun barmiki, yarinyar dakika kora tasamo miji sai bata rai kike" cikin fushi Momma tace "eh mijin da d'ana Shamsu yayi sanadi ba, da bai kaita ba da zata iya zuwa kampanin ne ita tama isa tashiga kalan wajajen nan, ni din ce dai sanadin duk wani good abu dasuke dashi a duniya" shiru Ummi tayi ta tsaya tana kallonta ganin bakin ciki karara bataso tabiyemata ayi fada gwara a lallabata ayi auren Ipy tace "to ki yakuri" tashi tayi tace "Salma tadawo ni natafi gida" tawuce tafita abinta Ummi tace "baki dauki komi a akwatin ba yakamata kisa albarka fa Adda" "Allah ya kyauta" tabude kofa tafice".

Wuraren 2 Safeerah suka dawo me gyara ta takirata daki tana rike da Waleed, Yasmeen da Salma tara da ita akwatinan falo suka kalla, kallo daya Safeerah tama kayan ta wuce, mesa yamata akwatina dayawa haka tawuce wajen me gyara tana ijiye Waleed gefenta dahar yatashi tace "ina zaka zauna kaga bari nabaka wayana" ta kunna mai cartoon a YouTube yana kallo aka bata maganin sha, Ummi tashigo dakin tace "Momma na so Salim yaje ya gaidata agida? Ki kira ki gayamasa" kallon Safeerah tayi saikuma tace "Ummi gaskiya ki gayamasa kedai"dakuwa Ummi tamata tace "kinci gidanku dakike cewa ni nakira, maza kirasa banson damuwan Adda please" tai maganan tana wucewa tafita, dan shiru tayi saita kalli Waleed tace "Waly bani wayan nayi kira kaji" cikeda rigima yace "uhn'uhhh" murmushi tayi tace "yakuri dan Allah, arama Ummy zan baka cheese" dasauri ya sakan mata wayan yace

"cheezee" gyadamai kai tayi tace "eh" takai wayan kunnenta harya katse bai daga ba sai gashi yakirata back ahankali ta daga tace "ina yini" muryansa kasa kasa yace "yakuke how is Waleed?" Ahankali tace "gashinan kusa da ni" murmushi yayi yace "basa wayan" zare wayan tayi daga kunnenta tasa a speaker tace "Waleed gashi

za'ayi magana dakai" karban wayan Waleed yayi yasa a kunne a juye da karfi yace "alooooooo" dariya Umma mai gyara tayi, itama Safeerah tai murmushi tana kalllon Waleed kaman zata cinyesa tana mugun son danta, daga ta dayan bangaren cikeda so Salim yadan daga murya a sigan yarinta yace

"Waleeeeddddd" zaro idanu Waleeed yyi saiya juyo yakalli Safeerah yaron yanada mugun wayau ga brain cikin voice nasa na yara yace

"Ummyyyy Abeeeeee!" Wani kunya Safeerah taji sau daya ta gayama yaron Abee by mistake but harya rike gyadamai kai tayi alamun eh shi ne, Waleed yasake juyawa yace "Abeee!" Wani piercing zuciyansa yanda yaron genuinely call him father yayi saiyaji yakara sonsa, cike da sincere love yace "na'am my Son, how are you"?

Dasauri yace "fine Abee" Salim yace "yesss good boy, how is Ummy"? Dan kunya Safeerah taji jin ya tambayeta, juyawa Waleed yayi yakalli Safeerah dake kallonsa ta batarai sosai yace

"Ummy fine Abee" sai yacire wayan yasa a kunnen Safeerah yace "Ummy Abeeee, talk" kaman Salim yagane me Waleed yayi saiyace

"Hello Ummy!" Wani irin sanyi Safeerah taji a kunyace tawani sunnar dakai murya kasa kasa tace "ni sunana Safeerah" dasauri Waleed yace

"Ummy!" Salim yayi murmushi mai sauti kadan yace "kinji ko Ummy, why did you call?" Cus yasan bata kira saida wani abu, ahankali tace

"ahmmm daman Momma Yayar Baba keson ganinka ta wannan gidan" shiru yadanyi he knows akwai yaro awajen ahankali yace "okay" yace "Waleeeeed" dasauri Waleed yacire wayan daga kunnenta yasa anashi yace "Abeee Ball" dasauri Salim yace "meya sami ball dinka"?

Dasauri Waleed yakalli Safeerah cus jiya ta karbe ball din ta boye cus ya buga a tv, raurau yayi da idanu kaman zai fashe da kuka yace

"Ummyyyyyy"idanu Safeerah ta zaro yanzu Waleed har ya iyakai karanta, ahankali Salim yace "don't cry zansa Ummy ta baka ball dinka bata wayan" sama Safeerah wayan yayi a kunne anatse yace "ina ball dinsa?" Ahankali tace "na karba na boye" "mesa?" Ya tambaya ba wasa, Waleed ta kalla tace "tv yake bugama kwallon" strictly yace "and so? Maza kibasa ball dinsa, seizing the ball is not a solution, he's a small boy he needs to play, correct him gently then kibasa his own space na ball, maybe back yard ko wani room is okay" sosai taji kalaman sa hakan yasa tace "okay" dasauri Waleed yamaida wayan kunnensa yace "Abeee" murmushi Salim yayi yace "Ummy zata baka but karka buga a tv is not good okay" gyadamai kai Waleed yayi yace

"okay Abeee" dan ijiyan zuciya Salim yasauke like is this how sweet kids are wallahi he loves the boy, ahankali yace "bye bye Waleed" raurau Waleed yayi da fuska da Umma mai gyara da Safeerah sukahau kallon yaro kaga yaro, sai kawai yafashe da kuka sosai kafin Salim yayi magana Safeerah tasa hannu ta karbe wayan ta katse ta harari Waleed dake kuka tace "daga mutum yayi magana dakai saikahau mai kuka bazaije yayi aikin gabansa ba? Idan kana irin halin nan bazan kara baka wayana kayi magana dash.....

." Ringing wayanta yahauyi Umma mai gyaran tace "wallahi shima yana bala'in son Waleed gashinan yakira, ki barsa mana yarone jibi yanda kika sakashi kuka yanzu" cikin kuka Waleed yamikamata hannu irin tabasa wayan nan daukan wayan tayi tamika masa ya karba yakai kunne dayake ta manta batasa a speaker ba but gani tayi yadena kukan yakai hannu yana share fuskansa saiyahau murmushi saikuma yahau dariya sosai, Safeerah sai kallonsa take batasan meyake gayama yaron haka ba dayake dariya, hawaye taji ya cicciko mata a idanu dasauri tadena kallonsa she's just feeing bad for Waleed, mahaifinsa ya tsanesa baitaba ganinsa ba rannan dayasan tanada ciki yakirata shi bayason ciki, data haihu an kirasa but still bayaso ko pure water mahaifinsa Waleed baitaba sha ba, look at yanda yakeson wani a matsayin uba wanin da bamatasan ko zai barta taje da Waleed gidansa ba, dudda yataba fada but batasan ko parmanent bane, taki maganan sabida ita duk inda zatasa kafa danta na wajen idan bai yarda ba yasaketa, maybe duk hiran na yanzu ne suna zuwa gida yafara wulakanta Waleed ko ta haihu ya banbance nasa yaran da Waleed it happens ai she's just feeling bad for the boy, kusan 20min yayi yana magana da Waleed sannan ya katse Waleed yabata wayan da kansa yana tsalle yana clapping.[4/19, 10:43 AM] AMINA KABIR CAP: EPISODE 47

Mama Safeerah ta kalla tana wani irin kuka tana mikewa, Mama da ranta itama yagama baci tace "ina tare da Babanki dari bisa dari, da hankalinmu da tunanin mu bazamu taba bari ki bata rayuwanki sabida Abbati dayaso karban rayuwan taki ba! Maganan banza kike yarinya, yaron da dagake har Waleed zai hada ya hallaka kike magana haka akai, stand up and follow mijinki we will get Waleed back have faith in Allah, bani mayafinta Maman Yasmeen" mayafinta Zainabu ta dauko takawo tazo wajen Safeerah dake kuka itama tana warwarewa dan yafamata tarage murya tace "trust us daughter, trust mijinki, yanzu u are not thinking straight, but Salim is your best weapon na samo Waleed uhmm" yafamata gyalen Zainabu tayi tabata takalminta mai kyau na akwati Safeerah tasaka tana kuka sosai tana kallon Baba, Baba yakama hannunta saiya bude kofa Salma duk taji ba dadi hakama Momma cus sunsan ayanda Safeerah ke son Waleed babu inda zata yarda taje without yaron, but Baba ya tursasata, motan Salim Baba yabude yasata agaba yarufe yataho gaban motan daidai Salim na fitowa daga gidan, matsawa gefe Baba yayi yace "Bismillah Salim" tahowa wajen Salim yayi kansa akasa anatse Baba yace "Salim ina mai baka hakuri bisa kalaman da Safeerah ta faffada acikin gida akuma gabanka, inaso kasan Safeerah yarinya ce yar kankanuwa, she is only 20, girman jiki ne kawai dakuma kaddaran dayahau kanta harta haihu this early, yarinyar ce data taso taga

kalubale daban daban arayuwanta, don't pay attention to abubuwan data fada bata da wayau kuma bakomi bace illa shirme" anatse Salim yace "I know Abba" shiru Baba yayi saiyakai hannunsa yakama na Salim yarike gam sannan yadaga kai yakalli fuskan Salim yace "Salim" dago kansa Salim yayi yakalli Baba ahankali, anatse Baba yace "harga Allah na yarda dakai na aminta dakai, Salim ga amanar Safeera nabaka amananta, ban yarda ka dokarmim diyaba kaji" Baba yayi maganan muryansa tayi rauni and sounding serious, girgixama Baba kai yayi, Baba yace "Safeerah nada shirme kome tamaka ka sanar dani zan bata kashi na hukuntata, ita kadai gareni dan Allah ka kulamin da ita, kamin haka kamin komi aduniya"gyadama Baba kai yayi, Baba ya fuzar da iska anatse yace "nasan yanda takeson Waleed amman inaso na gayamaka ko da munci nasaran karban yaron a musulunce yanda yafadi bai yarda yaron ya zauna gidan wani ba Waleed bazai iya zama daku ba saidai yadawo hannunmu" dan lumshe idanu Salim yayi yabude su ahankali yace "I know Abba, I will handle that, I want Waleed yataso karkashina da mahaifiyarsa" Baba yayi shiru yana kallon Salim wato Salim na son Waleed matuka ahankali yace "tom shikenan Salim na yarda dakai" anatse yace "Abba Waleed d'ana ne, please kada ka kara magana haka, everything will be fine, namaka alkawari I will bring Waleed back" yadan juya yakalli motan sannan ya kalli Baba yace "I promise you zan maida kukan ta farin ciki!" Wani sanyi Baba yaji azuciyansa Salim yace "Safeerah is not alone anymore, duk matsalolinta nawa ne and I will do my best to see na kauda damuwanta, Abba bawanda zan bari yayi hurting matana da raina saidai in bana numfashi! Just take care of yourself da Mama, Safeerah will be fine kaji Abba kaima kadena damuwa" wani kwanciya hankalin Baba yayi ya kama hannun Salim gamgam yanajin wani kaunarsa yace "nagode Salim je kutafi saida safen ku" sakin hannun Baba yayi yawuce yasa hannu yabude motan yashiga batare daya kalleta ba yaja kofan yarufe saiya kunna motan yayi reverse yayi kwana yaja motar yafita daga yayi reverse yayi kwana yaja motar yafita daga estate din yanajin kukan datakeyi har cikin ransa but baice mata komiba cus baida abinda fada no body can understand the pain of a mother especially yaron da tunda ta haifesa tana tareda shi sai yaune rana na farko da basa tare.

Kusan tafiyan 40min yakaisu har barrack, dudda she is crying baihanata ganin barikin sojoji ba, ga sojoji rututu sai saramai ake, yashiga ciki anyi tafiya sosai sukakai wani hadadden estate nasu aka bude gate ya shiga, yayi parking agaban block nasu batare daya kashe AC ba yayi shiru yana sauraronta, she's seriously crying though bawai ihun hauka takeba but yana jiyo sautin kukan he knows she's extremely sad, yakai kusan 10mins zaune a motan sannan yabude motan yafito yazagayo ta side din datake yakai kusan 10mins zaune a motan sannan yabude motan yafito yazagayo ta side din datake yakai hannu yabude kofan ko dago kanta batayiba balle ta kalleshi, calmly yace "let's go inside" kaman bada ita yayi magana ba dudda tajishi sarai wani bata mata rai muryansa yayi duk taji she's regretting auren, dabatayi ba da ba'a rabata da Waleed ba, mema yakaita tayi auren nan, kaddara kawai, ganin taki motsi yasa yakai hannunsa ahankali yakama hannunta dake kan fuskanta tana goge hawaye dasu dudda yaji wani irin shocking daya taba

